*BAYAN GANGAMI*

*NA UMMU HEEBBAT*

*MANAZARTA WRITES ASSOCIATION*

PG 1

Duk da irin tsohon cikin da yake jikina, bai sa na fa sa gudun da nake ba. Saboda ina yin sa ne domin ceto rayuwata wajen ganin na tse-rewa mugayen y'an ta'addarta da suka cimma garin mu. Hannuna rike da hannun yarona na biyu. Mutanen da muke gudu da su da yawa sun tsaya. Saboda wahala yasa na dakata da gudun da na ke yi a wannan dajin da muka kusa cimma wani kauye. Tsayuwata ke nan Yarima yarona ya fara kukan ƙishirwa saboda zazzafan zazzaɓin da yake jikin sa! Ganin babu wani sarki sai Allah ya sa ban nemi shawarar a bokan tafiyar ta wa ba, na sake daukar hanya domin na ƙarasa ƙaramin kauyen da nake hango wa ko zan samu ruwan da zan bawa yarima ya sha a wannan halin, tunda na san bani da ko biyar a irin wannan lokacin da muka riski kan mu. Kuma koda ina da ma ba mai sayar da ruwa a wannan yankin da muke ciki. Haka na ƙarasa bakin ƙauyen da yake dauke da gidajen da ba su wuce na ƙidaye su ba. Amma a binda na riska na bakin ciki sai da ya sa na ji cewa da ma ban bar garin mu ba na zauna a chan y'an bindiga sun hallaka ni. Saboda kowanne gida na shiga na nemi alfarma da su bani ruwa na bawa yarona sai su haɗe min rai su juya yare sannan suce ba suda shi. Tun ina ganin abin kamar wa sa har na kusa karaɗe garin dai amma amsa ɗaya ce. Jikin yarima na sha fa naji yadda ya sa ke dau kar zafi ga kuma yadda yake ta faman mai-maita ruwa a bakin sa, tuni ruwan hawayen da ke cikin na mujiyata ya fara tunbatsowa zuwa kan dan-damalin fuskata! Tashin hankalin shine ina za ni ? Baya zan koma da nake jin sautin bindiga har yanzu ko kuwa gaba zan ƙara na nemi ruwa ? Shin idan na yi gaba zan samu ruwan ko kuwa zan ta tafiya ne cikin daji har mu mutu a hanya da ni da shi? Tambayar da zuciyata take ta faman je fo min ke nan. Amma sai na dauki kawai na yi gaba a bina tunda Allah yana tare dani. Da wannan tunani na ɗaga ƙafata da ta yi min tsami na fara tafiya ina jan yarima yana biye da ni cikin ƙarfin hali saboda ƙarancin shekarun sa basu kai ya yi wannan tafiyar ba tunda gaba ki ɗaya shekarar sa shidda ne. Tafiya mai nisa mukayi har muka riski wani kauye na gangara cikin sa domin gwada sa a ta wajen neman taimakon ruwa ko zan samu. Cikin iko na Ubangiji matar ta bani ruwa na bawa yarima ya sha, wanda galabaita duka ta sanya shi ya

ke la amai a ta ke a wurin, domin  cikin sa ba komai. Cike da jarumta na zauna daɓas a wurin na janyo shi jikina na ce; " Yarima Allah ya ba ka lafiya, rayuwa tana cike da tashin hankali kai ma har Allah ya nuna maka yadda duniya ta sauya ina kuma wannan abin cikina da bai zo duniya ba, shi kuma ko ya zai sami duniya idan mun rayu." Na karashe maganar ina matsar kwalla.

Matar da ta ba mu ruwa ta ce, "Baiwar Allah kuyi hakuri daman kowanne ɗan Adam da tashi ƙaddarar sa a rayuwa."

Murmushin ƙarfin hali na yi kawai bance komai ba na kishin giɗe a wurin na kalli yadda yarima ya ke fidda wani irin numfashi mai tururi, zuciyata kuma tana tunanin ko ina su mamana suka fake a wannan lokacin .

Kallona matar ta yi kamar ta san abinda yake zuciyata ta ce, " Ina maihaifiyar ki  da sauran 'yan uwan ki?"

Murmushin ya ƙe na yi wanda ya fi kuka ciwo na ce "Ban saniba wallahi na rasa su na rasa kowa na wa a wannan lokacin, kawai fatana abinnan ya lafa na koma gida na ga halin da kowa ya ke ciki. Hatta babban yarona da karamar ɗiyata ban san a wacce duniya suke ba, saboda sun fita makaranta abin ya faru, shi ma wannan da kike gani rashin lafiyar sa ne ya sa bai ta fi ba.

Na kai ƙarshen zancen ina wani irin kuka mai tsuma zuciya .

"Kiyi hakuri in sha Allahu komai zai dai-dai ta ki koma gida.

Da irin wannan kalaman ta samu na daina kuka na samu nutsuwa harma ina tunanin tunda ƙarar harbe-harben ya lafa an jima zan iya ko ma wa cikin garin mu.

Sai dai wani abun mamaki ko awa ɗaya ba a yi da  yin shirun namu ba abu ya sake tashi sabo fil! Domin wannan karon harda irin manyan roket ɗinnan ake harbawa wanda kararsu kamar ta aradu, domin har haske suke bayarwa kafin su faɗi inda a ka je fa su.

Ga kuma yadda abin ya ke sake tun karo ƙauyen da nake, ganin Mutane da na bari a baya yuyu guda sun zo suna wucewa ya sa na gane cewa tabbas baya ba lafiya abin ya sake barkewa, da kyar wata mace ta na rike da yaronta ta tsaya ta min bayanin cewa ai 'yan ta'addan sun ce kowa ya bar yankin wurin zasu sanya bom saboda 'yan ta'adda shine ake ƙara yin gaba dan kaucewa wannan lama.....  Bata ƙarashe min batun ba a ka saki wani harbin da sai da dukkan mu muka zube gurin durƙushe! Wani irin murdawar da cikina ya yi a wannan lokaci sai da na zaci ko haihuwa ce zanyi.

Bamuga ta zama ba dan haka har ba fullatanar muka dauki hanya ta daukamin yarona wanda a wancan lokacin ma wallahi bani da tabbacin halin da yake ciki kawai dai ina ta fama da abin cikina yadda na ƙuda ta ke taso min a cikin dokar dajin da muke tafiyar kurame .

Jin ƙafafuwan nawa sun riƙe ya sanya min tilas na tsaya a wurin  tuni na durkushe bisa guiwata ina numfar- fashin wahala. Kadan daga ciki suka tsaya saboda tausayin halin da nake ciki wasu kuma sukayi gaba.

Mun tsaya ke nan wani jirgi ya zo yana faman shawagi a kan mu ga shi kuma zumbutun sa wuta ce jajir ya ke shirin fiddawa! Ganin haka yasa wasu suka kwashi gudu, na dubi bafullatanar da ta ke dauke da  yarima na ce ku gudu ku barni kar su kashe ku dan Allah! Wanda hakan ya yi daidai ta fashewar fayar haihuwa ga kuma jini ya yanko saboda abinda ya

ke cikina yake son fita duniya..........

PG 2.

Ganin ba wani sarki sai Allah ya sa na sa ke bajewa a wurin domin bawa yaron cikina damar fitowa duniya. Ya yin da su yarima suka yi nisa da gani na, haka kuma ya yi daidai da wannan jirgi ya fara shan manya manyan harbi da ga yan ta'addan Da ke gefe da mu.
Ba zan iya cewa na mutu ko ina ra ye ba! Saboda tsantsar firgici da kuma a zabar ciwon na ƙudar da ya ka ma ni. Amma duk da haka Sha wuya bai fasa zuwa duniya ba, sunan da na laƙabawa yaron cikina ke nan tun kafin ya zo duniya! Daidai haihuwar shi dai dai isowar yan bindiga wurina, cike da izza guda daga cikin su ya dube ni ya ce, " Ke ba ki tsorata ba ne da baki gudu ba?"
Cike da firgici na ɗago na mujiyata na dube shi, na rasa ma wacce irin amsa zan bashi, saboda na fahimci ba makaho ba ne kuma ya ga halin da na ke ciki, shin to kuma mai ya ke son na ce masa? Jin ƙarar wani abu mai kama da aradu cikin kunnuwana shine ya sani jin ina neman ma na fita a hayyaci na. Ya yin da shawuya yake ta faman zabga uban kuka jiki duk jini ga kuma cibiyar da ba ta samu Alfarmar rabuwa da shi ba. Ni kuwa daga wannan lokacin na zama sumammiya.

Ban san ya ta kaya ba na farka da ga doguwar sumar da na yi na ganni gefe guda kuma shawuya an raba shi da cibiyar . Ya yin da wata mata ke ta faman sa ke naɗe shi cikin tsumma take saboda yadda iska ta ke ƙaɗawa mai sanyi, kallon na tashi ya sa ta ce da ni "Sannu da zuwa wannan yanƙin na mu, muna farin ciki da samun yar'uwa, Allah ya raya mana tukur domin wannan shine sunan da shugaba ya ce na sanar Miki an saka masa."
Wani irin mashi naji ya chaki zuciyata da na ga no inda na ke, tuni na zabura daga kwanciyar da na yi duk da irin wani irin a zaba da na ke ji daga ƙasa na amma bai hana ni zama ba! Shin yan'ta'adda ne suka ta ho da ni? Ina yarima da ba fulatana? Ina mijina da zulfa'u ɗiyata ? Ina mamata da Abbana da sauran yan'uwana? Shin a wanne hali su ke idan sun koma gida sun rasani? Irin wannan tambayoyin na yi ta jifan zuciyata da su wanda bani da mai amsa min su, na sake cewa, Lalle BAYAN GANGAMI a kwai wata ƙura!!!
Domin ko ya ya ne tabbas a kwai wani tashin hankali da yake faruwa a baya. Ga kuma wanda zai faru a nan! Dan ko giyar wa ke na sha ba zan ra yu a wannan dajin ba ! Na ƙarashe maganar zuci tare da zubar wasu azababbun hawaye Masu zafi.
"Idan kin gama tunani zuci zaki iya kar ɓar Tukur ki ba shi nono ya sha kafin ya illata da yunwa."
Sautin matar ke nan da ya riski kunnuwana, ƙuru na mata ina ƙare mata kallo. Dan haka sai ta yi murmushi ta ce, " Na san kina mamaki ne a kan ya a kayi na san tunani kike ko, na sani

tabbas! Saboda ko wa idan ya zo sai ya yi wannan tunani ka fin magana. Amma ke na fi jin tausayin ki saboda ɗanyan jegon da ya ke gare ki.
"Tofa!" Ita ce kalmar da na furta a lokacin da ta gama kwararon zancen na ta. A fili kuma na ce, "Bani shi nan." Na faɗa ina miƙa mata hannuna.
Miƙomin shi ta yi na ƙarɓeshi ganin yadda ya ke tsula kukan wahala!
Cike da tashin hankali na San ya shi a nono ina jin ɓakin ciki idan na tuna na haihu ba a cikin ɗangina ba! Kuma ba wani na wa kusa! Saboda yadda muka ci burin shan suna nida yan uwana.
Yadda ya ke shan nonon yana zuƙarsa ya sani na ji wani mugun tausayi sa ya kamani, idan na tuna a gida ina haihuwa tun a asibiti na ke bawa yaro nono ya sha. Amma wai yau nice da haihuwa ban san ma adadin a wannin da na haihu ba tare da na kalli jaririn ba, bare a yi zancen shan nono.
Allah kaine gatana a wannan wurin da na fa ɗo, Allah ka taimake ni na kufce zuwa ga ahalina! Na karashe maganar zucin da zuƙar majina.
"Ya sunan ki."
Ita ce kalmar da ta faso cikin kunnena."

Kallon matar na yi na ce, "Sunana Kubra."
"Madallah Kubra ina Miki fatan alheri a wannan kwangon da zamu rayu abin da na ke son na ja hankalin ki shine, kawai kiyi biyayya a zauna lafiya . Saboda gidan nan a kwai mata dayawa da maza kuma kowa da mijin auren ta! Kuma ke ma na san kwanan nan zakiyi sabon miji."

Cike da fargaba da taraddadi na bude baki da hanci da idanu duka ina kallon ta! "Sabon miji kuma."
Na watsa mata wannan tambayar.
Murmushin ta yi ta ce "Tabbas! Kuwa domin mutum baya sati ake daura masa aure."

"To ai ni ina da miji kuma bamu rabu ba."

"Ke ki ka san haka, abinda na sani kawai ko wa ye mijin ki idan har kika zo gidan nan to kin gama auren sa!"

Tashin hankali wanda ba shida rana!!! Shine abinda na iya furta wa a zahiri.
"Na shiga uku ni Kubra ta ya zan auri wani bayan Nasir yana da rai kuma bai sake ni ba?"

Bata bani amsa ba jin motsin tafiyar mutum zai shigo cikin ɗan ke wayen.
Dan haka daga ita har ni mukayi gum da bakin mu, har ya shigo yana rike da wata zungureriyar bindiga wanda da za'a gwada tsayin ta da yaro ɗan shekara goma, to da tabbas zasuyi ɗaya!
Dogo ne kakkaura, mai ƙaton hanci da kuma wargajejen baki, ga shi ba fara'a. Cikin wata irin hausar sa kwaɓaɓɓiya wacce ba zan ma iya ga ne ainahin yaren sa ba ya ce, "Kausar! Ka sener masa da dokokin gida ko ya ya."

Matar da ya kira da Kausar wannan wacce ke tare da ni na duba yadda na ga tana ta faman

karkarwar amsa masa kamar haka, " O..oo OGA yanzu na ke ..na ke shirin sanar mata sabo......."
Bai bata damar ƙarasawa ba saboda wata uwar tsawar da ya daka mata, ba ita bama ni kaina sai da na yi dan karamin suman zaune, dan lokacin da na dawo hayyaci na na fuskanci shawuya bisa ƙasa abin sa, a she wai firgitar da na yi ce ta sanya shi ya wantsalo daga cinyata. Amma da ke ya ci sunan sa sha wuya ko kuka bayyi ba.
Ya ce , "Keeee mahaukaciyar ina ce!!!!!! Zaman me kike da ita tun ɗazun? To maza ki sa ta sanya ɗanta a inda zata San ya shi cikin jikin ta ki Kai ta gurin OGA gaba ɗaya."

Da to ta amsa masa cikin in ina har ta na yi tana russuna wa kamar zata hantsila.

Cike da mamaki na ke tambayar kaina " Wato bayan wannan ma a kwai wani OGA gaba daya? To shi OGA gaba dayan kuma da wacce siffa zan ganshi? Yau na shiga uku na lalace ga shi ya ce na sanya dana a inda zan sa shi, shin ba zan tafi da shi ba ne ko ya?.

Ashe duka maganar tawa ta fito fili,sai ji na yi Kausar ta ce, "Yana nufin ki sanya shi cikin hijabin ki ki ɓoye saboda ai ya tausaya miki ma, domin idan wani ko wata daga yankin nan suka ganshi to zasu iya cewa ya yi musu ki basu, kuma tilas ki bayar ɗin, domin gidan duk abinda ka ne ma kana samun shi."

Kamar wata so kuwa na zama a gaban ta na ce "Ban gane ba! Shin wai kina nufin shawuyan zan bayar wanda ko suna ba'ayi ba?"

"Tabbas haka ne maganar amma idan kina ganin wasa ne to ki gwada ki ga ko zaki dawo da shi idan bayyi wasu iya ye ba."
Ta mayar min da amsa tare da miƙamin wata hijabi mai kauri da girma.
Tsabar mamaki ma ban iya cewa komai ba, sai kuma na tuna maganar ta ta karshe na ce, " Na ji kince komai mutum ya ne ma yana samu ko?"
Kallona ta yi ta ce"tabbas haka ne."
Cike da jin daɗin amsar ta harwani saukar ƙaramin wani dutse na ji daga ire-iren duwatsun da suka sanya zuciyata ta yi min nauyi wani ya sauƙa da ga ciki. Cikin karsashi da zumudi harda wani karya murya na ce "To dan girman Allah idan muka je shi wa jen OGA gaba ɗayan ki nai mamin Alfarma a barni na koma gida."

Wata irin dariya ta bushe da ita wanda sai da na dauka ma ko tana da iska ne ko kuma iskar ce kanta sannan ta ce "Da ana iya samun wannan damar da baki zo kin samu kowa ba. Dan haka wuce muje kawai kuma kar ki kalli kowa bare wani ya yi yunkurin rabaki da yaron ki."

Tana gama fadar haka ta kama hannu na ɗaya muka fita ya yin da hannuna ɗayan ya ke rike da shawuya cikin hijabin.

Mutane iri iri ne zaune tanti tanti maza da mata kowa yana harkarasa da manyan bindiga,

mazan basu da kyan gani ko kusa. Tunawa da na yi da maganar ta na cewa kar na kalli kowa ya sanya na yi saurin kai kaina ƙasa.

Amma jikina yana bani ana kallon mu ko ina saboda yadda idanun jama'a suke yawo cikin jikina kuma daidai lokacin shawuya ya fasa wani irin kuka wanda ya ja hankalin jama'ar wurin duka suka dube mu har wani daga cikin su mai rike bindiga ya yi wani murmushi ya mike tsaye ya zuba min na mujiyar sa.

Cike da halin ni y'atsu na tsaya kamar wanda ƙwai ya fashe min a ciki ya yin da Kausar ma ta kasa gaba ta kasa baya. A zuciya ta na ce yau na shiga uku idan suka karbi shawuya kuwa tabbas zan mutu a gunnan!!!! Saboda shine kawai na ke da tabbas din cewa zan kallah a gabana tunda sauran ban ma san halin da suke ciki ba........ Wanda ya yi dai dai da sake hautsinawar sa a cikin shijabin.............

PG 3

Duk da irin tsoran da ya riski zuciyata bai sa na ƙi lallaɓa sha wuya ba da hannun da na ke riƙe da shi ba, sannan ta shin hankalin shine yadda wannan murguje jen ƙaton ya ke nufo mu.

Amma cikin iko na Ubangiji sai na ji wata murya daga bayan mu tana faɗin

"Ansar ga Zaid nan ya tashi ba madara."

Wanda a ka ƙira da Ansar kuwa ba kowa bane fa ce wannan wanda ya tunƙaro mu, sai naga ya tsaya yana cewa. "Ashe shine ke ta tsula kuka? Na zaci wani yaron muka samu." Yana fadar haka yana juyawa .

Aikuwa muna ganin ya juya muka dauki hanya ba tare da mun sake juyawa ba, duk da irin yadda zuciyata ta ke harbawa bai sa na kasa sauri ba har muka isa bakin wani katafaren wuri wanda ya ƙawatu da ado amma shi ma duka na tanti ne. Wasu zaratan maza ta ko ina a lamunsu masu gadi ne tunda kowa da makamin sa.

Haka muka dinga kutsa wa muna wuce su saboda bisa dukkan a lamu sun san da zuwan mu, dan ba wanda ya ce damu cikan ku. Tafiya mai tsayi mukayi cikin tantin kafin muka iske kofar shiga wurin OGA gaba ɗaya.

Shigar mu ke da wuya na hangi wata kujera irin ta juyawar nan, wanda ya ke zaune kuma ya juya baya, ga wasu zaratan maza daga gefen sa suna tsatstsaye da manyan bindigu masu shegen tsayi kowanne fuska a haɗe.

Cike da taraddadi na tsyaa ganin Kausar ta saki hannuna ta juya waje, cikin zuciyata na ce "Yau na ga ta kaina ya zata barni a wannan wurin da ba mace sai maza, ga manyan makamai ." Ina tsaka da jawabi da zuciya na ji wata murya cike da izzah da kauri kamar ta saraki ta ce, "Kubra! Ina Miki Barka da zuwa , Biyayya a kan komai waji bi ne, sannan kuma kada kiyi wasa

da rayuwar ki, ina nufin duk sanda kikayi yunkurin guduwa tabbas! Zan sa a kashe ki da kaina."

Wani irin ruwa ne ya cinye ne dajin
maganar sa ta karshe saboda firgicin kisan da na ji ya ambatamin, domin Ni kuma a tawa zuciyar bana jin zan bar ahalina na rayu a wannan wurin . Jin ruwan bai sake jiƙe min sawayena ba yasa na sunkuya, ashe fitsarin wahala ne tare da jinin haihuwa! Tashin hankalin shine ganin a babbar fadar OGA gaba ɗaya hakan ta faru.
Ganin irin kallon da ɗayan na tsayen ya ƙure ni da shi yasa tuni na durkushe a gun na ce, "Dan Allah kuyi hakuri ba da gangan na yi ba. Kuma na ji duka batun na sa sai dai......." Wata uwar tsawar da aka kirɓamin ce ta sanya Ni haɗiye maganata....

" Ke Kubra anan ba'a neman wata alfarma sai abin da aka ce da kai kawai dan haka ki kama bakin ki."

Kasa cewa na yi komai amma kuma tuni wani irin ciwon cikin bayan haihuwar nan da yake kama mutum ya murɗe Ni har na fita cikin hayyacina wani abun mamaki shine ina dawo wa hayyaci na na ganin bakin tantin kausar tana tare da ni sai dai kuma babu shawuya!
Cike da damuwa na ce "Ina yarona dan girman Allah."
Jujjuya kai naga kausar ta yi kuma ga wasu hawaye da suke son zuba daga idanun ta tana kuma toshe bakin ta saboda kar wani ya ji me zatace nie oho ban sani ba.
Na yunƙura na sake cewa, "kashe shi suka yi ko kuma ƙarɓeshi sukayi?"
Ita dai bata ce komai ba ta kama hannu na da niyyar ta jani mutafi amma ƙyam na jaɓe a wurin . Ganin haka ya sa wani dake gefe ya saki wani harbe wanda ban san sanda na gusa daga wurin ba .
Amma duk da haka tafiya kaɗan mukayi ina tuna shawuya baya hannuna na zauna na fashe da wani uban kuka mai cin zuciya harda birgima. Nan fa kallo yadawo kan mu......

Jejen fillo kuwa bayan abu ya lafa ne suka dawo da yarima ya gama galabaita ta sauke shi daga bayanta amma me, tana sauke shi ta gane a she ma gawace a bayan ta!  Tashin hankali wanda bashi da rana ai tuni fullo ta yi waje ta fara kurma ihu tana faɗin " jama'a ku she she ni yaron a mana ya mutu! Uwar shi ta bani shi na rike kar ya mutu ! Wayyo jama'a ku she she ni, na ce yaron ya mutu ku she she ni."

Jin kwarmaton ta ne ya sanya mutane da suke zaune gefe gefe domin jira zuwa anjima su shiga gari suga ya abin ya ke, sai suka taru a gidan, kowa yana shafa yarima abu ɗaya yake cewa ya mutu! Fullo kuwa banda ihu ba abinda take zabgawa. Hakuri aka shiga bata aka fara tunanin yadda za'ayi masa sallah mata suka zauna mazan suka fita waje.
Fullo ta sake komawa gurin yarima ta zauna ta rungume shi tana kuka ta ce "Yaro bance wa innarka zan bar ka ka mutuba ya zakamin haka do Allah. Haba yaro yau na shiga ukku!
Kamar a mafarki kawai yarima ya yi wata wawuyar ajjiyar zuciya wacce ta sanya fullo razana a guje ta miƙe tana faɗin "Aradu ya tashi bai mutuba daman yaro ba zai mutuba yatona min asiri ."

Cike da alhini mazan suka taru kansa suna masa addu'o'in da kuma zuba mushi ruwa a fuskar sa kadan kaɗan.

Cikin gari kuwa ba kowa sai wanda suka shigo daukar kayan su domin tafiya hijira dan haka duk wanda ka gansa dauke ya ke da akwatin tafiyarsa ko buhun kayan sa.

Chan sai ga zulfa'u yarinya ƙarama tana ihun kuka ta na cewa "Mama mama ina mamana ya yarima kajo ka ƙaini mama" Jin batun na ta ne ya sanya wani dattijo ya kalle ta ya matse kwallar da ke fita daga idanun sa haƙika dole ya dauki yarinyar nan, sai dai idan ya dauke ta mai zai bata shida bashi ko biyar a jikin sa? Kuma idan ya barta ya yi rashin hankali saboda yarinyar bata wuce irin shekara huɗu ba ɗinnan da
dai me wayoce, yanzu haka Allah yasan halin da iyayen ta suke ciki wajen ne manta . Hannu ya miƙa da zummar daukar ta kuma sai ya tsaya chak!! Kome ya gani ko ya tuna.........

PG 4

Ganin wasu samari sun tun karo shi ne yasa bai dauki zulfa'u ba, saboda yadda suke kallon ta suna murmushi kamar da sanayya a tare da su.

Da sallama a bakin su suka ƙaraso wurin tare da faɗin, "Baba wannan yarinyar ina ka same ta ? Kai ma sha Allah wallahi mun jima muna neman ta tun faruwar abin ga Chan baban ta shi ma ya bazama tun safe ."

Kallon su ya yi ya ce, "To bayin Allah wannan dai nima yanzu na ganta kuma ina shirin na dauke ta na ga tana kallon ku kuma kuna kallon ta shine ya sa na dakata da ɗaukar tata.

Amma na tausaya mata saboda yarinya irin wannan a wannan lokaci ai hatsari ne a ce bata tare da iyayen ta."

"Haka ne baba wallahi an sha wuya matuka ainun kasan da yake abin da ya faru lokaci guda ne shine fa kowa ya tarwatse. Amma bari na ƙira Nasir ɗin yazo ya ganta ko hankalin sa zai kwanta." Ya faɗa yana kara wayar sa a kunnensa .

Jim kadan naji ya na sanar da nasir ɗin cikin farin ciki. Aikuwa bai ɓata lokaci ba ya zo wurin, saboda ba nisa tsakanin inda suke da inda ya ke shiɗin.

Ita kuwa zulfa'u ganin su faruk ya san ya ta farin ciki domin faruk ƙani ne a wurin nasir dan haka tuni faruk ya rungume ta bisa ƙirginsa.

Koda nasir ya zo hannun ya mika ya karɓe ta ya rungumeta a ƙirginsa ya fashe da kuka ya ce, " Babyn mommy, yau na sa me ki jiya na samu haidar, amma kuma na rasa mommy da yarima...." Ya ƙarashe maganar yana sake fashewa da wani kukan kamar mace.

Baba tsoho ya du be shi ya ce " yaro hakuri zakayi wannan lokacin da muka tsinci kan mu a cikin sa kowa ya jijjiga! Amma abin da ya fi sauki shine mubarwa Allah komai mu miƙa lamurran

mu zuwa gare shi ."

Majinar kuka Nasir ya zuƙe ya goge hawayen ya ce "Haka ne na gode baba."

Da haka suka yi sallama suka wuce gida .

Kowa ya na zaune jungum-jungum kamar gidan ma koki . Ya Fido itace uwa a wurin Kubra sai ƙannen ta mata guda uku wato Maryam da Hadiza da basma. Sai kawu Bala shine uba a gare su wanda ya samo sunan ne daga yaran ƙanin sa da yake gida guda suke zaune.
Gefen ya Fido salame ce matar ƙanin kawu Bala sai goggo saratu surukar Kubra wato uwar Nasir da su faruk.
Lokacin da su Nasir suka shigo kowa sai da ya mike duk tunani su zasu ga har da Kubra zasu shigo, amma ganin su su kaɗai shine abin da ya sake kashe musu jiki, ya yin da Maryam da basma suka zauna daɓas a wurin don su ko kula da zulfa'u ma basu yi ba sun zaci ba'a samo kowa ba .
Jin ana cewa sannu zulfa'u Allah sarki yarin ya ba wayo sanann suka gane ashe an same ta .
Jin ana ambatar sunan zulfa'u ya sanya haidar fitowa daga ɗaƙin kaka saboda tun da a ka sa me shi ya ga babu su bai fitoba a ɗakin yana ta faman kuka.
Da gudun sa ya rungume ta ya fara kuka, "Babyn mommy mun rasa su mommy da yarima shike nan sun kashe mana su yanzu ba mu da mommy mukam .
Jin kalaman sa tuni Maryam da basma suka fashe da kuka domin kamar dama jira suke idanun su fal hawaye.

Saboda kaf cikin su ba mai kirkin aunty Kubra tana da hakuri duk da cewa tana da tsiwa amma bata barin su cikin damuwa, komai na su idan tana da halin yi tana musu, hatta ya Fido Kubra ce ke mata dinki lokaci bayan lokaci ita da baba.

Baba ya dube su ya ce , "Kuyi shiru in sha Allahu zata bayyana nan bada jimawa ba...." Ya faɗa yana sunkuyar da kansa domin shi kansa ƙarfin halin rashin ɗiyar ta sa yake, musamman idan ya tuna yadda take dauke da juna biyu haihuwa ko yau ko gobe.
Maryam ta ce, "Baba taya zamu iya dena kuka bayan ba musan halin da y'ar uwar mu ta ke ciki ba? Ga ciki jikin ta, yanzu baba idan aunty Kubra na hannun mugaye me suke mata a wannan lokacin ........tana kaiwa nan Nasir ya mike ya fice domin idan yana jin irin wannan batun zuciyar sa zata iya bugawa.

Haka suka yi ta kokawa har suka hakura suka koma zaman kurame.

Dajin su OGA gaba ɗaya

Kuka sosai Kubra ke yi na rashin shawuya amma ba shi ba zancen sa har kusan dare. Iya tashin hankali ta shiga ba kaɗan ba! Saboda ji take kamar ta haɗiyi zuciya ta mutu .

Kusan shida na yamma wani mai fuska a rufe ya shigo tantin na su yana rike da shawuya ya mika mata shi bai ce ƙalaba ya juya.
Cike da farin ciki ta ke kallon sa amma kuma ta kasa bude shi saboda firgita! Saboda ji ta ke kamar gawa ya kawo mata.
Tunawa da yarima tuni ta yaye mayafin da yake rufe ta ga yana bacci abinsa cikin kwanciyar hankali.
Ajiyar zuciya ta sauke, Amma kuma yau gaba ɗaya hankali ta ya karkata zuwa ga a halin ta! Ji take yau dole ta je gida ko ta wane hali dan haka ta ƙudirci niyyar yau cikin dare dole ta san abinyi wajen tserewa duk da bata san ko ina ba.......

Cikin dare kowa ya kwanta masu tsaro sun baje bindigu ta ko ina saboda su basa bacci haka aikin su yake sai dai da safe ga kuma yadda macizai ke kai kawo a wannan dajin .

Amma duk da haka bai hana Kubra ta goyi shawuya ba ta su ɗaɗe ta fito a tantin cikin bakar abaya, saboda kausar ta tafi gurin mijinta ita ma.    Cikin sanɗa take tafiya  abin da  tana duba gaba da bayan ta . Har tayi nisa da tantin saboda yadda take bin lunguna, sai dai kash jin saukar wani abu a wuyanta tuni ta daskare a wurin ta kasa koda motsin kirki ..........

PG 5

Jin wani abu mai sanyi ya naɗemin wuya shi ne yasani suman tsaye don tuni zuciyata ta hau dakan luguden uku uku. Sanyi da santsin abin shine ya tabbatar min da cewa maciji ne! Cike da tashin hankali na ƙame wuri guda dan lumfashi ma da ƙyar na ke sauƙewa.
Jin yana tunƙarar hayewa kaina ta baya na fasa wani gigitaccen ihun da ya amsa kuwwa a wannan dajin, har na mance mai ya fito dani.
Kafin kace Kwabo tuni wasu zaratan maza masu ɗauke da manya bindigu suka kewayeni tare da haske min fuska. Hannu ɗayan ya sa ya kama macijin dake jikina ya jefar tare da tarwatsa shi da albarushi.
Ƙarar albarushi ce ta sanya shawuya fasa ihu shi ma, jin haka ɗaya daga cikin su ya ce, "Wato guduwa zakiyi ko? Ashe baki da hankali! Ance Miki ɗan gida ma yana iya fita a wannan ƙauyen ba tare da an masa Rakiya ba bare ba ƙo?" Cike da fargaba na ke sauraran maganar sa mai kama da tsawar aradu a kunnena.

Tsawar da ya sake jefamin ce ta sanya Ni tilas na yi magana .

" Ba gudu zanyi ba kawai na rasa yadda zanyi da yarona ba shi da lafiya yana min kuka shine na fito nai man taimako. " Na tsara masa wannan ƙaryar da bansan sanda ta shiryuba cikin

ƙirjina.
"Wuce munafuka ko me ne ne ma dai zamu haɗu watarana idan gudun kike niyya ma,kuma kinsan dokar gidan nan duk wanda muka kama da niyyar gudu kisa ne. Kema kawai na Miki uzuri ne saboda baƙuwace ba don taausayi ba!"
Kamar wacce ƙwai ya fashewa a ciki haka na dawo tantin da na bari na zauna ina rafsar kukan bakin ciki.
Sai yaushe zan kufce ne a wannan wurin? Ya Allah na ina yarima ina zan ganshi, duk runtsi jikina yana bani ƙila zulfa'u suhadu da Nasir ko a mace ko a raye. Ya Ubangiji na yarima fa? Ta faɗa tana sake fashewa da kuka.
Ya Ubangiji yarima yana cikin wani hali na gudun ceton rai na barshi, Allah kasa yarimana bai mutu ba ya rabbi idan yarima yana raye Allah ka sa da shi da ahalina su samu rangwame na rashi na.
Da ire-iren irin wannan tunani bacci yayi nasarar saceta durƙushe da goyon shawuya.

*Dajin Fulani*

Yarima zaune yana ta muzurai da idanuwa, Fulani zaune gefen sa tana bashi fura amma yaƙi karbar furar.
Ta ce "Yaro do Allah ka sha fura kaji. Kuma ka faɗa min suna mamarka sai na kaika gida na san yanzu tana chan tana neman ka." Jin ta ambaci gida tuni ya buɗe baki ya kurɓi furar yana ruwan hawaye ya ce. " Sunan ta Kubra muna ce mata mommy ."
"Yawwa yarona kaifa ya shunan ka to do Allah ." Fulani ta faɗa saboda bazata iya tuna sunan da ta ji mamarsa ta na faɗa masa ba.

"Yarima." Ya furta a taƙai ce.
"Yawwa yarima yarona yanzu anjima zan shirya idan munje shikin gari sai ka hiɗi mani sunan anguwar ku na kaika."
Kai kawai ya girgiza ya sake gyara zaman sa idan ya tuna mommy sai ya fashe da kuka saboda ya san ta mutu tunda ya ganta da jini kuma ga jirgi da yan bindiga sun kusa gunta suka gudu

Fullo bata hana shi ba saboda tasan dole ya yi kuka duk da cewa yana yaro amma sarai ta san bazai mance komai ba.

Misalin biyu na rana ta fita ita da yarima suka fita bakin titi ta tare musu abin hawa suka shiga gari .
Garin da har yanzu ko kwatan kwatan jama'ar da suke ciki basu bayyana ba.saboda gaba-daya sunyi hijira duk kan wanda ya ke zaune yana zaune ne dan bashi da wurin zuwa ko kuma dan ya rasa wani na shi yana cigiya.
Tunda suka shiga yarima yake hawaye kuma wani lokaci ya yi murmushin fullo ta dube shi ta

ce " Ina ne unguwar ku?"

"Jar ƙasa kofar samu naka." Ya bata amsa cikin tsananin son yaga ya gansa cikin gidan.

Basu yi wata tafiya mai nisa ba saboda basu da nisa da in da suka sauka.
Suna zuwa ƙofar gidan su ba kowa dan haka yarima ya kwace hannun sa daga wurin fullo ya afka cikin gida yana faɗin daddy na dawo ina mommy?" Amma shiru dan haka sai yarima ya tsaya ƙyam! Yana mamakin jin shurun ina jama'ar gidansu? Sabon kuka ya fara yi ya juyo sukaci karo da fullo ta ce Ko ba nan ba ne gidan?"
"Nan ne basa nan dai ina ga duka sun mutu ne ya faɗa yana fashewa da kuka."
Suna tsaye fullo ta rasa abinyi sai wani bawan Allah ya zo wucewa dan unguwar ya gansu ya ce da su ai duka mutanen gidan suna gidan kakan su ƙanin mai gidan ne ya bude yanzu amma ban san inda ya tafi ba.

Koda yarima ya ji haka kawai bai tsaya cewa komai ba ya kama hannun fullo tiryan tiryaan sai gidan kakan su.

Yana zuwa ya shiga da gudun sa ya yin da fullo ta ke biye da shi domin wannan karon bata tsya baya ba.
Ganin sa da sukayi ya sanya duka suka mike daga zaman makoki da suke
Wasu na kukan farin ciki wasu na murna da dariya chan ya Fido ta ce "yarima ina ka baromin mommyn ka?"
Jin wannan tambayar tuni ya yarima ya sake fashewa da kuka sabo, ganin haka Hadiza ƙanwar Kubra ma ta rungume shi cikin kuka ta ce "Sanar da mu ka ji yarona kaji."

Da hannu ya nuna fullo wanda sai sannan suka ganta . Wurin zama aka bata daga bisa aka nemi ƙarin bayani daga gare ta .
Itama kukan ta fara kafin ta fara basu labarin haɗuwar su da Kubra da rabuwar su tana kai ƙarshen labarin Maryam da Hadiza suka sume. Nasir kuwa sake maimata kalmar ƙarshen ya ke " Haihuwa a dajin kuma ga yan bindiga?"
Ganin yana neman zauce wa yasa malam ya zaunar da shi, gida duka ya dauki kukan mutuwar kubra domin su sun bata mutuwa ne kawai.

Hakan kuwa shine yayi dai dai da zuwan dogarai uku suka ce da kubra ta
zo a daura mata aure ..........,.

Cike da firgici na sunkuyar da kaina yayin da zuciyata ta ke min luguɗen dakan ɗaka, saboda ji nake kamar zata tsaga ƙirjina ta fito ga wani azababben zazzaɓi da ya riski dukkan gabobina lokacin guda!
" Aure kuma!" Kalmar da na furta cikin zuciyata, wanda yayi daidai da uwar tsawar da ɗaya daga cikin su ya sa ke je fa min.

Ciki da damuwa na yunƙura na miƙe na goya shawuya muka dauki hanyar fadar OGA gaba ɗaya.

Zuwan mu ke nan na hangi maza shida gefen kujerar sa dukan su durƙushe a gefen sa. Yana nan yadda na barshi ranar ma kamar baya tashi saboda yauma bai juyo ba,wuri na samu na durkushe kamar yadda na ga sunyi.

Kamar saukar wahayi haka muke jin sautin Muryar sa cikin sanyi ya ce. "Na so a daura auren kina kusa amma kuma rashin isowar ku da wuri tuni har an gama komai. Dan hakan ku bata kudin sadakin ta da kuma goron ta ku nuna mata mijinta akai ta gidan ta . Allah ya basu zaman lafiya."
Tunda ya fara maganar na ke jin wani irin zugi yana saƙƙowa daga cikin zuciyata har zuwa cikin cikina da ya kewani irin murɗawa. Ganin abin da na ke ganin sa kamar wasa yana son zama gaskiya ko na ce ya zama ma shine ya ke sake je fani cikin ruɗani!
Jin takun mutum kusa dani ya sani saurin ɗagowa daga sunkuyar da kan da na yi ƙasa. Sai ya ce dani "Ga wannan kudin sadakin ki ne kamar yadda OGA ya faɗa ga kuma goran ki. Sannan wanchen mai ɓakin kayan shine miji a gareki  dan haka ta shi muje a ra ka ki gidan ki." Tunda ya fara bance komai ba kuma ban kalli wanda ya nuna min din a matsayin mijin ba saboda bana bukatar hakan, hannu na sa na dauki kuɗin da goran  na miƙe domin bin umarnin su.
Ganin na miƙe ne yasa duka suka miƙe suka sanya ni gaba saboda sumin rakiya. Haka muka ɗunguma tafiya mai nisa da fadar OGA gaba ɗaya chan wani tanti suka kaini wanda ya fi na wa girma da kuma kayan aiki cikin sa na bukatar mace. Murmushin ya ƙe na yi wanda ya fi kuka ciwo na ce cikin zuciyata "Harda wasu kayan aiki wato ga yar iska mara sanin addini."
Ganin na tsaya ina tunani ya sanya ɗaya daga cikin su ya ce ki shiga ciki anjima ango zai zo da kayan amarchi.

Ban furta ko kanzil ba na shiga ciki na zauna ina faman sauki lumfar-fashi.

A chan kuwa gida da ƙayar a ka shawo kan su Maryam suka farfaɗo daga sumar da sukayi .

Shi kuwa Nasir wani irin kuka yake mai tsuma zuciya idan ya tuna da Kubrar sa da irin zaman da sukayi na amana yadda ta ke mai biyayya a gare shi. Amma ace irin wannan rabuwar zasuyi? Ai gwanda ace shine ya mutu ya barta da ya fi masa sauki. Ko kuma ace mutuwa ta yi sukayi mata sallah suka binne to da zaifi samun sukunin da rashin sanin tabbas.

Wannan abin shine abinda ya fi ƙo na masa zuciya. Ganin halin da ya ke ciki ne ya sanya MLM ya zo wurin sa ya dafa kafaɗar sa ya ce . "Nasir rayuwa fa daman cike ta ke da ƙalubale mai tarin yawa, saboda ba dukkan yadda kaso kayi rayuwa ka ke samun yi ba.
Komai kuma da kake ganin yana faruwa ba wai dan an tsane mu ba ne , A'a sai dan a jarraba imanin mu. Dan haka ina son ka dauki wannan jarabawar da ta riske mu, a wannan lokacin na san dole zaka ji zafi amma idan ka tuna cewa komai Allah ne ya ke tsara shi to tabbas zaka samun nutsuwa a zuciyar ka. Kuma ka yawaita ambaton Allah a koda yaushe hakan zai sanya ka samun nutsuwar zuciya.
Da wadannan kalaman Nasir ya samu ya ji wani irin ƙarfi ya riski zuciyar sa tuni kuma a wannan lokacin ya fara ambaton sunan Allah kamar yadda MLM ya ce da shi.

Mama fedo ce zaune da yaran na ta a barandar da ke gaban ɗakinta.
Hakuri ta ke sake basu ya yinda idanunta suke zubda hawaye saboda tabbas ta yi babban rashi a cikin yaranta idan har ya tabbata Kubra ta bar duniya.

Mafi girman tashin hankali kuwa shine ace tana raye amma basu san inda zasu same ta ba. Shin ta ina zasu fara ya kuma zasuyi da yaranta domin kullum sai sun tambayi ina mahaifiyar su, illah yarima da yasan inda ya barta . Shi baya magana sai da adukkan lokacin da ya tuna ba shida wani aiki sai na kuka.

Misalin shabiyu rana zulfa'u ce zaune a cinyar Basma ƙanwa ga Kubr. Ta ce "Aunty Basma idan mommy ta dawo zan koma wurin ta saboda na jima ban ganta ba kuma ina son ta haihu na yi gaɗa." Jin kalaman zulfa'u sune suka sanya zubar hawayen basma a ɓoye. Saboda ɗazu mama ta yi musu nasiha cewa su daina kuka sai addu'a, kuma sun yi mata alkawarin haka .
Ta ce "zulfa'u yarinyata mommy zata dawo nan ba da jimawa ba, kuma zaki koma hannunta har sai kince inzo in dauke ki. Gaɗa kuma kamar kinyi in sha Allahu saboda mommy zata baki abun yin idan ta dawo ɗin." Ta karashe maganar cikin ƙarfin zuciya, saboda yadda idan ta kalli yarinyar ta ke sake bata tausayi.

Kowa ya watse a garin a wannan lokaci sai wanda sukayi saura irin su family Kubra da suke zaman tsammanin ko zasuji labarin ta.
Amma jin wannan labarin shine ya sanya malam yanke shawara da su bar garin na wani lokaci. Tunda har yau sojojin sun hana su zaman nutsuwa dan tunda abin ya faru suke musu ihu bayan hari! Dan motsi kadan Zasuyi ta harba roket masu girma suna musu fargar jaji tunda abin ya riga da yafaru to abar jama'a su zauna lafiya mana! Kuma hakan da suke yi ne ya sa duk wani mai son zama yake barin garin.

Ko da yaje musu da wannan batun basu ƙi amincewa ba domin gwanda su bar garin su huta da tashin hankali suji da damuwar inda zasu ga Kubra a mace ko ra ye.
Nasir dai kawai ya amince ne amma har cikin zuciyar sa kuwa baya son ya bar garin ba tare da ya ga kubra ba.
Amma haka suka hada kayan su domin tafiya maihaifar kakannin su

Domin su huta zuwa wani lokaci.

Kubra zaune ta tafka uban ta gumi ta ji mutum ya shigo ba ko sallama da wasu ledoji a hannun sa ya ajjiye su gefen ta ya ce " Ki dauki Wannan sune kayan amarchin da ake bayarwa a wannan dajin kuma ki sanya a ranki nine shugaban ki idan kina son zaman lafiya ."

Jin batunsa na yi dole ma na bashi amsa tunda daga ni sai shi kuma banga wannan zarbaɗediyar abar ba wato bindiga, daman ita na ke tsoro dan haka na ajjiye shawuya gefe na mike cike da ƙarfin hali ina muzurai wai dole Ni gani jaruma na ce " Ko taya zanyi biyayya a cikin wannan auren?"

Kallo na ya yi cike da mamaki ya furta " Ban fahimta ba."

Sake gyara tsayuwa nayi "Ina nufin aure kan auren da a ka min, taya ina da miji kuma yana raye bai mutuba zan zauna da wani a matsayin miji ?"

Dariya ya bushe da ita ya ce, "Kubra!! Wannan doka ce kuma dole ki bi kuma kowa haka ake masa daga lokacin da kika shigo dajin nan idan kina da aure to auren ya watse saboda ke a matsayin sabuwa kike a wurin."

Wani malolon taƙaici ya riski allon ƙirjina har ya fara min zugi na ce " To kuwa gaskiya bazan iya zaman nan ba saboda Ni ban taɓa jin wannan lamarin ba sai yau. Kuma bazan taɓa hada jiki da wani ba har sai auren da ke tsanani mu ya inganta." Cike da harzuƙa ya dube ni ya daga hannu ya shimfiɗa mini wani mari Mai zafi wanda sai da na ga wasu taurari suna ya wo.

Ba shiri na durƙushe a wurin ina mai zubar da hawayen damuwa .

Kallon ta ya yi ya ce zan baki lokacin ki yi nazari kafin na zo na karbi hakkin aurena, na Miki haka ne kawai dan na ga kina jego .
Kuma agidan nan ba ki da damar guduwa saboda ko da kin gudu to akwai inda idan harkinje ba hanya sai koguna, kuma mutanen mu ne suke tsallake kowa da umarnin mu! Dan haka zaɓi ya rage na ki. Ko kiyi biyayya mu yi zaman aure ko kuma ki gwada guduwa ki shiga hatsari kamawa, kuma aka she ki........ Yana gama fadar hakan ya kwance ya juya mata baya a kan ƙaramar katifar da yake.
Wani irin yanayi ta ji wani abu na son bugeta ta Sume saboda tashin hankalin da ta ke ciki.
"Allah ya rabbi ka kawo min sauki cikin wannan uƙubar da nake ciki.....

PG 7
Ganin ko ya kula harma ya fara baccin sa hakan ya sanya na tashi daga zaman da na ke na dauki buta na yi alwala duk da cewa ina cikin halin jego. Amma hakan bazai hanani zaman yin

addu'a ba, dan haka wuri na samu na zauna na fara kai kukana wurin mahaliccina saboda shi ka ɗai ne zai fidda ni ga wannan ukuɓar dana ke ciki.

Tsawon lokaci na dauka ina zubar hawaye gaban Allah ina sanar masa damuwata sai na ga shawuya ya farka na shafa addu'o'in na dauke shi. Nono na fara bashi yana sha ina kallon sa hawayen idanuna suna zuba kan fuskar sa. Da yanzu muna gida da yana cikin net killace cikin kayan sanyi ga yan'uwa sun kewaye mu. Zanci kaza na sha shayi mai kauri na gyara jikina da ruwan zafi! Amma tunda na zo sau ɗaya naga idanun ruwan zafi, abinci kuwa iya ka abincin gado ne wato wake da shinkafa sai su taliya suma kuma duka masu yaji ne.

Gari na wayewa ya kawo min kayan abinci masu yawa a cikin harda kayan miya dakuma kifi bushashe. Banyi wasa da rayuwata ba na ajjiye komai a gefe tunda na sanar da mahallici na nasan zai tseratar da ni.

Dan haka na zage na daura ruwan zafi na na juye cikin wata kula na daura girki na na dafa taliya da miyar ja wadda ta ji kifi, bayan na sauke na sake daura wani ruwan .

Ruwan kular na juye rabi na yiwa shawuya wanka tas farine tas da shi ga idanuwa ma sha Allah kamar na Nasir dan yana matukar kama da shi.
Sauran ruwa na ɗiba na shiga dan zagayen da na gani na shiga gayar jikina ba karamin wahala na ci ba saboda gaba daya na yi tsami kasancewar ba kulawa tun farko na sha a zaba kawai daurewa na ke da na fito na samu ruwan ya tafasa shi ma sai na juye cikin kular na sake daura wani na janye wutar saboda ina samu ina kama ruwa da shi wannan na kular kuma shi ne zan dunga sha.
Ina so na samu ƙarfi jiki na warware sosai ta yadda zan iya jurewa dukkan wata wahala da zan fuskanta a wajen guduwa dan na ci alwashin tse re wa. A binci na zauna na ci na ƙoshi na sha ruwan ɗumi nan danan kuma ruwan nonon ya fara malalowa domin daman ni daga na haihuwa ba wani jinkiri nono yake zuwa. Dan haka na ki shingiɗe har barci ya yi awun gaba dani abinka da mai jego ba za'a rasa gajiya ba.
Kusan kwana shida muka dauka haka har mun fara sabawa da zama wuri ɗaya domin na lura yana da sanyin hali ga kuma ba shi da yawan zaman gida, ranar da muka zauna gida ɗaya muka kusa yini muna dan taɓa hira sai ranar na gane ainahin kamar sa. Fari ne dogo mai tsayi ga jiki gare shi dai dai gwargwado. Ba shi da muni amma kuma bashi da yawan fara'a ya ɗan bani labarin sa saboda ya ce mun mata ɗaya ya taɓayi bai sake wata ba sai yanzu.
A raina na ce wannan ɗin ma baka samu mata ba. Daga gare ni dukkan yadda ya so ya ji wani dan labari ban ba shi ba na kance masa na mance komai nawa. Satin mu guda ya fara fita dani bayan gari da nufi na sake da shi domin na lura shi acikin y'an ta'addan ma yana da tausayin mace mai jego .

Kowanne na miji yana fita da matarsa yawan shan iska har bakin ruwan da suke faɗa harma wani lokaci wasu suna hayewa domin su samu sakewa da matansu. Kullum mukaje wurin ina lura da dukkan wani motsi saboda na samu hanyar kufcewa. Amma abin ya fi ƙarfin tunani na

saboda mugun tsaron da yake a wannan dajin ! Haka na ke lallaɓa rayuwata ina ta ka tsan-tsan da komai.

Abu na farko da ya fara daga min hankali shine yadda wannan mijin nawa da ban san sunan shi ba ya fara neman hakkin auren sa a gare ni! Na shiga damuwa da firgici da na fahimci lamarin, saboda a tunanina zan samu wata damar tserewa kafin ya amfana
dani.

Nasir ne zaune bakin gadon su da Kubra idan ya kalli kayan ta da yake ajjiye a kan gadon wanda ta goge ta ce shine zata sa gobe suje gidan Hajiyar sa. Wani hawaye Mai zafi ya ke zubarwa idan ya tuna yadda sukayi rayuwar su cikin farin ci da ƙaunar juna.
Baya mance ranar da ta ke ce masa idan ta haihu tana son su koma wata jahar daban da zama domin ta gaji da rayuwa a wurin da ya ke da fargaba
Duban ta ya yi ya ce "Haba ƙurraty na, ai komai kika ga ya faru to rubutacce ne shi. Dan haka ko ina zamuje idan har Allah ya tsara wani abu zai faru ba fata ba to tabbas sai ya faru."
Kallon sa ta yi cikin yanayi na sanyin jiki tace " Haka ne Habibi amma wallahi sam wannan garin ya fita a zuciyata saboda wallahi bana son abinda zai tarwatsa min zuri'a ko ace na rasa ka ! Saboda ina matukar kaunar ka Habibina yadda baka tsammani.
Murmushin na yi dajin batun na ta na karshe na ce "Haba ƙurratul aini na, Ba sai kin fa ɗa ba na fi kowa sanin haka kuma in sha Allahu ba abinda zai faru."
Sake gyara zaman sa ya yi bayan ya dawo daga duniyar tunanin matar sa ya dauki kayan ya sanya cikin durowar kayan ta ya rufe ya yi maza ya fita a ɗakin domin komai zai iya faruwa da shi idan har yana kallon dukkan abin da ya shafeta.

"Ƙurraty! Allah ya bayyana min ki in sha Allahu baki mutu ba."
Nasir ya faɗa yana share hawayen idanun sa.

Ganin kwana biyu ya matsa da zancen ne na buƙaci da ya zo muje wani ƙauye mana to domin muma musha amarchin mu Chan tunda haka ne. Bai yi musuba ya amince min, kuma na sanar da shi na fison ƙauyen da sai an tsallake ƙogi saboda na ga duniya Nima.
Ya ce dani ba damuwa gobe na shirya mutafi.

Hakan kuwa ta kasance tun safe na ke shirin fita saboda ni kadai na san me na shirya cikin zuciyata
Kamar misalin ƙarfe goma na safe ya zo ya ce dani Bismillah,dan haka muka dauki hanya muna tafiyar ƙafa har zuwa bakin ƙogin da yake da ta zarar ba nisa ba ce sosai a wurin su amma kam

zai kai kamar kilo mita guda da rabi.
Koda zuwan mu ya sanar da su inda zamuje ba su hanamu ba suka sanya mu cikin kwale-kwale ya yin da wani farin cikin ya riski zuciyata don ji nake komai ya zo karshe.

Amma mai zai faru tuƙawa biyu akayi na ji wata murya mai sauti cikin amo ana cewa "Ku dakata!! Ku dawo da su!!!!!.............

PG 8

Wani irin yanayi na ji ya ziyarci zuciyata kamar zan zauce. Saboda koda wasa banyi zaton wani zai kawo min cikas a cikin wannan tafiyar ba.
Shi kansa wanda ake laƙabamin da sunan mijin nawa maganar ta bashi mamaki sosai. Saboda yadda na ga yayi sakwato da baki.
Ganin masu kwale kwale sun juya suna mayar da mune yasa na ji cewa shike nan haƙata bata cimma ruwa ba.
Koda muka koma bakin ruwa sai cewa ya yi shi wanda yayi ƙiran ke nan, "Baka bani shaidar fita ba, ko kuma baka da wata shaidar zaka fice ne." Nida ban san kan komai ba sai na tsaya ina kallon su.
Saurin sanya hannu ya yi cikin aljihun sa har yana kyarma ya ce, "Dan Allah kayi hakuri tabbas nayi laifi kuma idan OGA gaba ɗaya yaji zai dauki mummunan mataki a kaina. Mance wa na yi sam gaba daya."
Wata irin dariya ya bushe da shi kafin ya ce " Baka da matsala da ni, banga laifin ka ba koda ka mance da kanka ne saboda dukkan wanda ya mallaki mace kamar wannan tabbas ya gama samun rayuwar farin ciki.
Asha amarci lafiya."
Murmushin gefen baki na yi cikin zuciyata ina ayyana yadda zanyi kawai.
Shi kuwa mijin nawa ce masa ya yi godiya na ke shugaban mahayan ruwa.

Da haka muka dauki hanya cikin taf ke ken kogin da ya ke da faɗi da tsayi! Kuma ga nisan tafiya sosai har sai da na ƙosa kuma na fara jin jiri saboda yadda ruwan ya ke juyawa.
Amma da yake sannu sannu bata hana zuwa sai dai a jima ba aje ba. Dan haka dai gamu bakin karshen ruwa mun samu hayewa. Hamdala na yi bayan mun sauƙa y'an kayan da ya dauko a matsayin kayan zaman amarchi su ya dauka muka sauka baki daya da su. Sai dai nan ma fa akwai tsirarun y'an ta'addar masu shigar da mutane sai kuwa wasu da matan su kamar dai yadda muka fito.
Nesa sosai ya yi damu saboda na lura baya son hayaniya dan haka munyi nisa da su yadda ko ɗuriyar su ba ma ji bare gani.
Hakan kuma ya min da ɗi.
Wani karkashin wata bishiyar da bansa me ce ce ba muka zauna muka ajjiye kayan mu ya sauke bindigar sa ya ajjiye ta a gefen kayan, ya samu wuri ya kwanta ya ce dani "Wuta zaki hada ki dafa mana abinci da ruwan wanka kafin dare ya yi miki domin yau ɗin nan zaki bani

haƙƙina ko ni ko ke cikin dajin nan.

Wata fargaba ce ta riski zuciyata amma da na tuna Allah sai na ji na samu ƙwarin guiwa. Na kalle shi na ce, " Yanzu ina zan samu makamashin hada wuta a wannan dajin?"
Idanu ya daga ya kalle Ni ya ce " Ki zaga baya kadan zaki samu kirare sai ki dauko."
Idanu na zaro kamar da gaske na ce "Kai ! So kake a sace maka ni? Taya zan shiga wannan kwararon neman kirare?"
Zaune ya tashi halamu ya harzuƙa da tambayar tawa " Ke ni barci zanyi! Waya ce Miki ana sace mutum a wannan wurin duk wata tafiya ƙalilan jama'ar mu suna nan sun yada Zango, dan haka ki saki jiki ki yi abin da ya ke gaban ki kafin lokaci ya ƙure miki." Ya faɗa yana jan tsaki tare da ko ma wa kwanciyar sa ya juya min baya.

Kunto shawuya nayi na sanya shi a nono ya sha ya ƙoshi na bashi ruwa na mayar da shi. Jin gurnanin mijin na wa ya yi bacci ya bani damar daukar wata ƙaramar gora mai dauke da ruwa na sanya ta cikin goyan ta gaba na ɗaure kyam! Na sake sanya wasu zanin na sake daure wa . Ban ma tuna ta batun cewa mutanen su suna gaba ko kuma ta ina zan fara ba, na kalle shi na masa kallon karshe ina jin wata irin faduwar gaba tana kai ko mo cikin zuciyata!

Amma wani ɓarin na zuciyata cike ya ke da jajircewa.

Dan haka na sanya gabana
yamma na fara takuna cikin hanzari bana tuna komai sai Allah da na ke ambato cikin bakina.............

PG 9
Hanya guda na dauka ba ko fargaba tafiya na ke cikin sanɗa kamar wacce ƙwai ya fashewa a cikin ta. Kusan tafiyar minti talatin na yi kafin duhu ya fara shiga na magrib amma kuma ban ga kowa ba ban ji motsin komai ba, dan haka sai na fara sauri gudun wani abu ya faru tunda na san makoma ta a wannan lokacin idan an ka ma ni.
Chan na yi nisa da tafiya na hago wani haske gaba wanda yasa zuciyata bugawar tara-tara a maitan na sha kwanar wata bishiya domin kaucewa wannan hasken.
Amma me zai faru ji na yi kamar na sake kai kai na wajen wani hasken na sake saurin boyewa cikin wasu ita tuwa ina kutsa wa zuciyata cike da fargabar kar shawuya yayi min kuka a wannan halin da na ke ciki! Ta cikin ita ce na ke sanɗa da ya ke akwai hanya na ke ƙurɗa ɗawa ina bi ina sake ni sawa da tafiyar. Chan kuwa yana farkawa yaga wayam ba ni ba labarin girki dan haka ya sake kishin giɗa yana faɗin lalle wannan ba ta nai mi zaman lafiya ba, yau zata sha wuya hannuna alƙur'an
Jin shurun ya yi yawa ne ya sanya shi leƙa ko wanne saƙo da lungu amma ba ni ba a lamuna cike firgici ya rasa abin yi, dan haka sai ya fara kwaɗamin ƙira amma shiru . Hakan ta sa ya fasa wata ƙara da ta amsa ƙuwwar dajin kuma dukkan wanda ya yi haka an san akwai matsala. Dan haka tuni zaratan maza suka bayyana dauke da makamai cike da ɗinuwa ya ke sanar musu da rashin gani na dan haka tuni suka afka dajin domin nema na.

Banyi aune ba naga na fita daga duhuwar kuma ba hasken dan haka ƙafa mai naci ban baki ba ai kuwa na rufa da gudu saboda kar wani ya haske ni ba wurin ɓuya. Ina ta faman gudu na ji na afka cikin wani rami wanda zurfin sa zai kai gaba uku na rijiya .

Allah yaso ban faɗi kan goyon ba, ganin haka sai na ji kamar na samu wata dama ce da zan huta a wannan wurin.

Sauƙe goyan na yi na sanya shi a nono bawan Allah tuni ya chafke ya fara sha . Wasu guntun hawaye ne suka zubo min daga na mujiyata saboda na san dole akwai masu bi na. To amma ya zanyi na fita cikin ramin nan ba tare da taimakon wani ba? Kuma dukkan wanda zai taimake ni tabbas sai dai masu nema na.

Jin sautin tafiyar wasu runɗuna suna faman mita cikin wani kalar yare yasa na ƙandare daga gefen ramin na gama yanke kauna da rayuwar duniya domin tabbas na san kamani za su yi ! Kuma laifina kisa ne kai tsaye, salati na fara domin samun na ga na cika da kalmar shahada.Nan da nan nafara jin sawayen su suna tsaye bakin ramin suna cewa da harshen Hausa.

Duk inda ta ke ka tabbatar kun ne mota ba tausayawa ko a wanne hali kuga ganta ku aiwatar da hukunci yadda ya ke.

Wata murya na ji kamar ta wanda ake ƙira da mijina ya ce " A'a Sadau su ka wo ta wuri na nine ya kamata na dauki matakin a hannuna saboda tsantsar yaudara da cin amana da ta min ."

Haka ne Barde na ji amfada da kakkausar murya .

Sun jima suna saƙa da warwara ɗaya daga cikin su ya ce yanzu mene ne abin yi a wannan lokaci? Ga dare ya yi ga bamu san ta ina ta ke ba tunda ba wani labarin ta bakin tafƙin da jama'ar mu suke.

Haka ne kam inji Sadau.

Yanzu kuje baya ku zauna ku kuma kuyi gaba dan haka nida Sadau a bakin ramin nan zamu waye muka ta ina zata tsira .

Wani irin murɗawa cikina ya yi nan take wata gudawa ta so kufce min amma Allah ya rufa asiri bata fito ba, wani irin zafi jikina ya ɗauka ga wani tururi da yake fita ta maƙo gwarona yau kam na san ta wa ta ƙare. Ban damu da rayuwata ba kawai na damu da shawuya ne dukkan gudun da nake ina yi ne domin sa, da ni kadai ce wurin su zan zauna. Amma ba zai yiyu na haifi ɗa daga tsatson daraja ya ra yu cikin y'an ta'adda ya zama ɗan ta'adda shi ma.

Kamar rawar aradu haka na ji wata murya na faɗi shugaba munga wata a lama a baya mu afka. Ai kuwa tuni na fara jin sawayen su suna komawa baya cikin ƙaraji da hucin son haɗuwa dani.

Suna tafiya na fara tunanin yadda zanyi na fita domin dama ce na samu na tsere daga hannun su tunda sun koma baya, amma abin takaicin shine ya zanyi na fita........

Ganin sun ta fi kawai na fara tunanin mafita yadda zanyi kamar wa ha yi na fara kai hannu na ji akwai irin ramuka ƙananu ta ciki dan haka na kama su na ke takawa kamar mai hawa tsanin ginin haka har Allah yasa na fito da kaina bakin ramin. Ganin ba kowa na yi saurin fitowa sai dai duk jikina ya yi min tsami ga yunwa ga jikin jego, tunawa da nayi da irin uƙubar da zata sa me ni a wannan wurin idan ban bar sa ba shine ya sanya na ji wani irin ƙwarin guiwa ya zomin. Tuni na fara tafiya ina sauri sauri gudun faruwar wani abu har na yi nisa da wurin . Na yi tafiya mai nisa kafin na iske wata bishiya wacce ta ke da ci ya yi busassu a ƙarƙashin ta. Dan haka nan na zube na zauna ina sauke lumfashin wahala tao kuma yunwar da  ta ke sake ta so min kamar zanyi amai. Kuka na fara ina tambayar kaina tambayar da bani da amsar su.

Shin sai yaushe zan fita a wannan dajin da babu wani a lamun titi ko abin hawa ?

Wa zai ce ce ni a cikin wannan dajin?

Me na yiwa Allah da haka ta ke faruwa dani?

Wacce irin ƙaddara ce da bazata same ni ba sai da na ke cikin wannan yanayi na jego ga yaro ƙaramin bai san kansa ba?

Haka na yi ta faman tambayar kaina abin da bani da amsar su. Sake goge hawayena na yi a karo na barkatai, ina tsaka da wannan tunani na hago wasu motoci da hasken su ya ke ba mai yawa ba suna nufo ni, tuni na mike na gudu bayan bishiyar na goya shawuya a bayana.  Kamar jira suke na buya suka hasko wani Haske mai yawa ya mamaye dajin kuma motar ta na tunkaro inda na ke amma ta gefen hagu na.

Har sun kusa wuce ni motar su ɗaya ta tsaya, cike da masifa ɗayan ya kurma wani mahaukacin zaki ya daki bayan motar ya ce  "Oga wannan motar fa ta samu matsalar dan bazata ta shi ba yanzu gaskiya sai zuwa safiya."

Wata murya na ji ya ce "  To yanzu mene ne abinyi ke nan?"

"Kwana ya kamamu fa oga."

Dariya ogan ya yi ya ce " Baka da hankali ke nan me zai sa mu kwana anan wurin da tsakanin mu da hanya bai wuce kilo mita biyar ba, kuma kasan jami'ai zasu iya biyo mu tunda sun ga inda mukayi. Dan haka kawai mu sanya wa motar bom mu barta a wannan wurin idan sun zo ta sheƙe su garin bincike ."

"Haka ne Oga ka kawo shawara dai dai kuma ya batun tsare hanya domin kama matar barde da aka sa mu?"

Jin kalmar sa

ta karshe ce ta sanya na saki wani fitsari a tsaye wanda ban san ina jin sa ba ma har haka.

Shiru na wani lokaci na ji ya ce "Da safe sai mu koma amma yau kan ba koma wa saboda a kwai yuwar su biyo mu."

Ni dai ina tsaye kamar gawa a gefen daman su. Daga idanuna na yi na hangi wani ƙasurgumin maciji ya nufo Ni daga jikin bishiyar da nake ra ɓe. Kuma idan na yi gigin matsawa tabbas zasu ji motsina saboda ciyayin da suke ƙasa.

Haka ina ganin macijin yana tun karo ni, tuna wa da maganar wata tsuhuwar layin mu nayi da ta ke cewa idan maciji ya hau kan ka baka motsa ba to bazai cutar da kai ba. Saboda zai dauka yana kan bishiya ne.

Dan haka tuni na dauki wannan Shawarar tunda wuri ya ƙuremin dan har ya hau kaina . Haka na daskare wuri guda har ya bi jikina ya sauka ƙasa, kuma Haka ya yi daidai da tashin motocin su sunyi gaba.

Suna tafiya kuwa nima na ce banga wurin zama ba tunda har da su bom.
Dan haka na dauki sabuwar hanya ina ɗin gisa ƙafata da ta min tsami. Tafiya na yi iya tafiya wacce ban san iyakar ta ba, dan har farin wata ya fara haska sararin samaniya.

Kwatsam na tsinci kaina cikin wani lambu na tumatir.

Aikuwa abin nema ya samu wai matar soja ta haifi dan sanda , zama na yi dirshan na fara cikin tumatir din nan kamar an aiko ni har sai da na ji na ƙoshi tukun na bari.

Guntun ruwan gorar na dauka na sha na ajjye na koma gefen lambun da baka jin sautin komai sai na kukan tsun tsaye haka ne ya tabbatar min da cewa a kwai tafki kusa ko kogi.

Dan haka na yanke shawarar na kwana a nan gudun kar na je na afka cikin ruwa!

Ina zaune na sanya sahwuya gabana saboda na sumto shi daga bayan na kwantar shi kan abin goyon, sai kuma na fara aikin nawa wato kuka saboda yadda idan na tuna cewa a wannan lokacin kowacce mace tana ƙrakashin kulawar mijin ta ne shi kashi yaron komai talaucin gidan su yan zu yana sanye cikin kaya da kuma shinfiɗa mai laushi! Amma ban da mu da muke talatainin dajin ga kuma fargaba.
Na ƙarashe maganar ina rushewa da kuka mai tsanani, ban san iya lokacin da na dauka ina tunanin ba har bacci ya dauke ni, ban farka ba sai waje asuba dan haka banyi ƙasa aguiwa ba na dauki guzurin tumatir saboda gaba na goya shawuya muka dauki hanya saboda bai farka ba

bare na bashi nono ya sha .

Na yi tafiya mai nisa har gari ya yi haske ban tsayaba a dokar dajin, kawai na ji kamar sautin takun wani abu yana bin bayana cike da firgici na juya cikin tashin hankali na ke kallon abinda na kalla wanda ya sanya ni yin na dama da guudwar da nayi....

PG 11

Zare idanuna na yi sosai saboda daman Allah ya albarka ce ni da manyan mganai, dan haka cike murya kakkaura irin yadda na ji su Barde suna yi na ce "Mu bil adama zaku yiwa haka? To idan ba ku maida mu bakin titi ba tabbas kun gama zama gawa da kuda ayyukan ku."

Shiru ya yi tunda na fara maganar yana ɓari sai da na sake masa wata uwar tsawa sannan ya ce cikin in ina...

"A yi ha ha ƙur rrri dan Allah ku kuke ganin mu ba mu muke ganin ku ba, wallahi nidai ban taɓa kowa ba a wannan dajin saboda Ni kaina a tsorace na ke aikina."

"Kai!!!!! Dakata min me ka ke yi a wannan dajin na mu ."

Na faɗa cikin ƙwarin guiwa.

Yana karkarwa ya ce idan ba damuwa ya ke jinnu kiyi min rai mu bar wurin nan kuma koda y'an ta'adda sun bayyana, to ki ɓoye ni idan ina baki amsar......ya ƙara durƙushewa a wurin .
Jin ya ambaci sunan y'an ta'addan tuni hanjin cikina ya kaɗa na ce " Ba zan boye ka ba!! Sai dai ka yi ƙoƙari ka kai mu inda ba zasu gan ka ba domin ka bani amsa .....amma da zarar sun bayyana anan zan Barka... Na faɗa ina kwashewa da dariya kasa kasa gudun ko suna kusa su jini

"Muje ya ke bil jinnu."

Shine abinda ya faɗa kawai ya yi gaba cikin farin ciki na bi bayan sa domin ina tunanin haka ta ta cimma ruwa.

Tafiya kaɗan mukayi muka shiga wata shimfiɗe ɗen lambun na yalo wani kewaye kamar ɗaki muka samu muka tsaya ya kalle ni ya ce.. "Anan muke fake wa kuma ba sa zuwa nan ."

"Kai ya shafa." Na furta ina fadin me ka ke yi a dajin mu da har kuka kashe mana goɗiya?"

"Ranku ya ɗaɗe wallahi Ni mai aikin lambu ne kuma ban san komai a kan kisan ba ."
Kallon sa na yi cike da gajiya a jikina kuma ga shi bana so na nuna masa tsantsar gajiyar da ta ke tare da ni saboda kar ya fahimci ni ba aljana ba ce.

Sai na ce masa "Ba ruwan ifriti da maganar ka!!! Abun da ya ke bukata kawai shine ka kaini cikin garin ku da ya ke kusa wanda diyar godiya ta bayana ba zata gaji ba a ya yin ta fiyar. Kuma kar ka bari wani bil'adama ya ganmu haka yana da ga cikin abinda zai jawo ka rasa ranka !!!!! "

Sunkuyar da kai ya yi ya ce cikin in ina "in in Allah ya ya yarda ba zasu gan mu ba ."

"Ka tsira!! ." Na furta haka cikin ƙaraji.

Juyawa ya yi domin mu tafi na fakaice shi na cire yalo uku na boye cikin kaya na. Muka dauki hanya ta cikin wasu lunguna da motoci ma baza su iya bi ba kuma mutum ma da kyar yake kutsawa. Lallai irin hanyar nan sai wanda ya santa kaɗai ne zai ga ne ta.

Munyi tafiya mai nisa na fara hango bakin titi kuma da wani gari chan gefen sa sai na ga kuma ya tsaya ya ce "To ya ke bil jinnu anan matsalar ta ke kuma. Saboda anan kam dole bil'adama zasu ganni.Ya faɗa yana russunawa.
Na ce da shi " Babu wata matsala! Muje kawai ...."
Koda muka fara shiga garin sai na fuskanci cewa garin ba babban gari ba ne ƙauye ne kuma ba shida wani girma.
Dan haka muna kaiwa wajen gidaje na ce da shi "Dakata! Anan zamu rabu, dan haka ka juya ka koma kar kuma ka sake ka wai wa yo! Yin hakan yana nufin kana wasa da rayuwar ka ne."
Da to ya amsa min ya kama hanyar dajin da muka baro ba ko waiwaye dariya na ji ta kubce min wanda rabon da na yi ta inda ta nutsuwa ce na irin wacce na yi da sunan aljana ba tun ranar da zamu rabu da mijina. Ba zan mance ranar ba kam tabbas.

Yana kishin gide ya ce dani. " Ƙurraty na, na ɗago idanuna na dube shi na yi masa kyakkyawan murmushi na ce "Na'am hubby."

"Ƙurraty wallahi ina sonki ɗayawa ranar da zaki haihu kawai na ke tunawa idan na tuna da yadda mata suke shan wuya a wajen haihuwa, wallahi ƙurraty sai na ji kamar na karɓa miki saboda bana son na ganki kina shan wuya." Ya ƙarashe maganar tashi yana langwabar da kai .

Murmushin na yi na kalleshi na bude baki " Allah sarki mijin ƙurrat haka Allah ya tsara mana mu mata karka damuwa muyi ta addu'a Allah ya kawo ta da sauki ."

"Haka ne ƙurraty amma gaskiya ba zan iya tsayawa a asibiti ba wannan karan dan haihuwar zulfa'u kusan kuka na yi , ke na yi ma saboda bayan kin haihuwa na dunga hawayen da ban

san na me ne ba."

Murmushin sosai na sake masa ƙasan zuciyata kuma ina farin ciki da alfaharin irin yadda na samu miji mai sona har tsawon wannan lokaci da na haifa masa yara uku zan yi na hudu bai rage wani abu da yake na soyayya ta a zuciyar sa ba.

" Karka damu hubby in sha Allahu zan haihu lafiya lau kana bacci sai dai na tashe ka ka ga yaron ka ko yarin ya ......

Wuri na samu na zauna bayan dawo wa daga duniyar tunanin da na afka ciki tabbas na san yanzu mijina yana cikin wani hali. Haihuwar da yake mata fargaba yau ta zo min cikin wani halin da ko ni ba zan iya cewa ga irin yadda na sha a zabar ba. Saboda sawun Giwa ya take na Raƙumi.

Ganin zaman ma ba shida amfani ya sanya na ta shi na dauki hanya na sake kutsawa cikin kauyen ina tambaya har na isa gidan mai gari .

Na nemi na gana da shi aka ce min sai zuwa sallar Ishaa na dare zai dawo .

Haka na zauna na ci yalo da tumatir na bawa shawuya nono  ya sha bawan Allah duk ya rame sai yanzu na ga asalin ramar da ya yi har sai da na yi ƙwalla saboda dukkan wani ƙashi na jikinsa kana ganin sa za ne, har wani ƙaton kai ya yi . Lulluɓe shi na yi na rungume shi acikin jikina ina faman sana'ar da ta zamo min abin yi wato kuka. Sai naji an dafa kafaɗa ta baya, saurin juyawa na yi na kalli wata baiwar Allah ta ce min kije fada mai gari ya na neman ki. Tsabar damuwa ban san ma sanda daren ya yi ba har suka yi sallah da yake ina cikin halin jego ba ni da damuwa a kan sallah amma fa ina bukatar kama ruwa domin duk jini ya ɓata min jikina har ya bushe idan ban da ƙarni ba abinda na ke yi.

Alfarma na ne ma wurin matar ta kuma amin ce min na shiga daga cikin gidan ta na wanke jikina na kama dukkan inda na san ya ɓaci na wanke na baza zanin ya ɗan sha sannan na daura shi may fito muka dauki hanyar fadar garin koda na je wurin a cike ya ke da jama'a kamar za'ayi wani taron, shiga ta ke nan na hangi wannan bawan Allan da ya taimaka min ya shigo dani gari . Yana ganin fuska ta ya mike ya na nuna ni, luuuu ya zuɓe kasa sumamme!

"Tashin hankali!" Shine abinda na furta a bakina ya yin da sauran jama'ar wurin duka suka yo kaina suna faman salati da salallami suna faɗin mai kika masa baiwar Allah?

Daga zuwa wuri .

Nidai na yi zuru zuru na kasa cewa uffan ga kowa....

Wani irin kallo jama'ar wurin suka bi ni da shi dukan su,hankali na ya yi matukar tashi na fara ƙokarin yin magana domin na kare kaina.

Mai gari ya ce da ni " Ke baiwar Allah! Daga zuwa har kin fara jefo mana masifa! Wacece ke? Daman kune irin tsofin Mayun nan na cikin daji da kuke bibiyar al'umma kuna lamushewa? To ahir ɗinki tabbas kin zo wurin da zaki karɓi hukunci dai dai da abinda kika aikata.

Tunda kalaman bakin sa suka fara furzuwa zuwa masarrafin jina tuni hantar cikina ta yi muguwar kaɗawa, har wani jiri na ji yana neman ɗi ba na.
Na so ace mutuwa ta zo min nida shawuya a wannan lokacin ko zamu huta da wadannan tashin hankalin .
Kuma da na san cewa haka zata faru da mu to da kawai zan bayyana kaina a lokacin da y'an ta'addan suka bayyana a wurin bishiyar nan .

Amma sai dai kash! Bakin alƙalami ya bushe baya bata dawo wa.
Durƙushewa na yi duka a ƙasa na ce.

"Wallahi ban san wannan maganar da kake yi ba, kuma bani da alaƙa da ita.

Hasali ma da zaka ji labarina da zaka......." Tsawar da ya daka min ce ta sani tilas na shanye sauran maganganun bakina. Sai ya ce,

"Muna fuka bamu nemi jin komai daga gare ki ba, dan haka ki kama bakin ki sake yin wata magana anan wurin tamkar ƙara wa kanki laifi ne.

Shirun dole ce ta riske ni bani da wata mafita sai wacce Allah ya kawo min.

Yarima ne zaune ya haɗe kai da guiwa yana tunanin mahaifiyar sa. Fedo mahaifiyar Kubra ta dube Maryam ta ce Kinga Maryam lamarin yaron nan kullum damuna ya ke wallahi, kar ya je wata cuta ta kama shi. Damuwar da ya yi ko yayan sa bayyi ba.

Maryam ta yi murmushin da ya fi kuka ciwo ta ce " Mama dole ya ka sa mancewa saboda waya san a irin yanayin da ya ganta , kuma mama tunda kika ga ƙarancin shekaru irin na yarima ya kasa mance wa da wannan lamarin wallahi mama aunty Kubra ta shiga wani mummunan yanayi kafin su rabu..... Ta ƙarashe maganar cikin kuka saboda daman neman kukan ta ke yi.

"Haba Maryam yanzu mene ne abin kuka saboda Allah bayan kuma ke ce wacce zaki rarrashe shi. Amma kuma kina yi a gaban sa ta ya shi kuma zai samu sauki a cikin zuciyar sa?"

"Mama zan kiya ye." Ta furta a chan ƙasan maƙoshin ta.
Miƙewa ta yi jiki ba ƙwari ta nufi inda yarima ya ke ta ɗago da kansa ta rungume shi ta ce "Yarima yarona kayi hakuri in sha Allah mommy zata dawo kuma ba abin da zai faru da ita."
Ɗago rinannun idanun sa ya yi ya ce ; "Aunty Maryam sunyi mata rashin adalci kuma sai na je na ƙarbo ta! Aunty Maryam ki taimaka ki sani a ajin sojoji dan Allah na koyi yaƙi na je na ga ni ko sun kashe min mommy ko tana wurin su." Ya faɗa yana durƙusawa a gaban ta.

Cikin raunin zuciya ta dube shi tace ; "Tashi yarima zan kai ka in sha Allahu kaji, amma ina son ka de na sanya damuwa sosai a ranka saboda idan ka kamu da cuta to bazasu kar ɓe ka ba suma sojojin a wurin aikin na su.

Jin ta ambaci ba zasu ɗauke shi ba tuni ya ɗan saki fuska ya ce "To aunty indai zasu dau ke ni na je na dawo da mommy na daina daga yau."
Murmushin ta yi ta kalle shi "Yawwa yarona haka na ke son ji."

Suna tsaka da hirar sai ga zulfa'u ta shigo da gudu hannun ta dauke da Sweet tana tsalle ta ce cikin gwarancinta, "Atti na, baba ya bani Sweet ba jan baki ba mommy zan ajjiyewa."
Dariya Maryam ta yi ta ce "Shike nan ɗiyar mommy wato ni bazaki bani ba ko? Ai bazan Miki wanka ba gobe ."

Tsalle ta fara yi tana shirin kuka tana cewa "Bana sho ni wanka zaki mun gobe na je ba mommy sweet!" Ta faɗa tana maƙe kafaɗa.

Janyo ta Maryam ta yi jikin ta ta rungume su duka su biyun .

Yayin da mama ta ke gefe tana kallon su cikin tausayawa har sai da ƙwalla ta fito mata ta yi saurin goge wa..........

PG 13

Suna rungume jikin ta Nasir ya shigo gidan, kallo ɗaya ya yi masu ya gane halin da suke ciki dan haka cikin sauri ya saki hannun yayan yarima wato haidar ya juya waje saboda tabbas idan ya tsaya sai yaji hawaye zai zubo masa .

Haidar yaro mai Shekara goma sha huɗu. Ya dube su ya ce "Aunty Maryam har yanzu ba su dena kukan ba?"
Daga masa kai tayi a lamun basu dai na ba.

Kallon su ya yi ya ji wani mugun tausayin su ya kama zuciyar sa, sai dai ba yadda zayyi da

lamarin tunda haka Allah ya tsara musu sai ya ce da su.  "Dukkan wanda ya sake mana kuka ko mommy ta zo ɓoyeta zan yi nida daddy muna ganin ta bazan kawo ta wurin ku ba.
Jin ya ce haka duka suka ce "Yaya haidar mun daina ka yi hakuri."

"Yawwa yaran mommy to na ji, kuyi murmushi na gani ."

Murmushin suka yi suka kalle shi shi ma ya mayar musu ya ce "To kuje wurin kaka fedo ku zauna ku bar aunty Maryam ta huta kunji ko."

Kai suka kaɗa suka wuce shi ma ya je ya gaida kakar su ya shige dakin sa.
Zama ya yi a bakin ƙaramin gadon da ya zama wurin kwanan sa tun ɓacewar mommyn su, duk da cewa yarima ya ga halin da mommy ta ke amma bai kai shi damuwa ba saboda yadda mahaifiyar su ta ke nuna musu so da ƙauna duka ba wariya farin ciki ya  wanzu a familyn su a lokacin da mommyn su ta ke nan. Saboda shine yaro na farko da suka haifa tunda ya ta shi bai taɓa ganin faɗan su ba bare hayaniya, kuma kowanne a cikin su yana nuna masa so har ya kai ya samu ƙanne mommy bata daina sa shi jikin ta ba kamar yadda daddy ya mai da shi abokin sa .  Saboda yana ganin hakan shine zai taimaka masa wajen kula da tarbiyyar sa.

Ko abinci na safe da dare dukan su  suke haɗuwa su ci a babban faranti .

Jingina kansa ya yi da bango ya daki bangon yana wani irin kuka mai tsuma zuciya. Ya ce " Allah ya wadaran sojojin garin mu da suke zaune kamar mata a zo a ci garin da kuke tsarewa da yaki har a dauki ganima amma ku ka sa komai!!! Yau da ni soja ne a yau zan ɗibi zuga na baza  dajin da aka san suna nan muyi bata kashi na duba uwata!!

Mommy kina ina!!! Ina zamu ganki mommy kewarki ta kama mana zuciya mommy, idan kin mutu mommy ko gawarki a kawo mana mugani!!!"

Ya faɗa cikin ƙaraji da ihu dan ya mance yanzu ya gama yiwa ƙannen sa faɗa.

Dukkan abinda ya ke faruwa baba Bala ya na bakin ƙofar ɗakin zama ya yi dur shan yana hawaye ya kasa shiga dakin ya rarrashe shi.

Kubra ta since goyon ta ko zasu ga ƙaramin goyon su tausaya mata, amma da suka zo mai gari yana ganin sawayen ta ba faratu ya kaɗa baki yana riƙe haɓa ya ce "Wato da maitar ki ta motsa kika rasa abin ci sai kika cinye fara tanki.

Bari yanzu zamuyi maganin ki yana gama faɗa ya na ƙiran wani mai suna Yakubu da ya kawo barko no da wuta a turare ta da shi .

Jin abinda ya ce yasa ta figita ta gigice ta ce  cikin kuka " Dan girman Allah komai zaku mun karku haɗa da wannan yaron da bai san komai ba a duniya ko baku tausaya min ba to ku tausaya masa. Ku rike shi idan kun gama min hukun ci sai ku bani ."

Ina gama fadar hakan na ga duka sun ja da baya wata mace gajeruwa daya gefe ta ce , "Allah Ya tsare mu riƙe yaron mayya, salon Ya je ya cinye mu wato mu rike shi shike nan kin samu dama, to baki isa ba. Ai ke ba abin tausayi ba ce! Mayyar mace ai muguwa ce.

Dan haka me gari mafi sauki abin da zamu mata shine a bude ƙasan ta a watsa mata yajin zata yi bayani da bakin ta ita mayya ce ko ba ita ba ce.

Kallon ta duka jama'ar da ke wurin suka yi suka ce tabbas wannan shawarar ta yi kuwa maza kuyi mata aiki cikin gaggawa kafin ta ƙame mana bakuna da ƙafafu!

Ai kuwa suna jin haka suka afka kaina suka wangale min zanin ya yinda duka mazan wurin suka juya baya suka watsa min wani yaji .

Wata irin ƙara na sake ta a zaba ga jego ga barkwano har suma sai da na yi domin azabtar da Ni da suka yi sai dai Allah na yi ihu kamar zan zare shawuya yana na shi ihun ina ji amma ba damar daukar sa .

Saboda na kasa zama na kasa tsayuwa kuma awannan halin suka yo kaina da tambaya suna cewa mayya ce ke ko ba ita ba ce .

Tsabar azaba da masifar da na ke ciki na san idan na ƙaryata hakan wata azabar Zasuyi min na ce "Mayya ce tabbas na jima ina cinye mutane!""

Salati suke baki dayan su suna tsine mun aka fara kawo ruwa ana kuzamin ina sake yin wani ihun, ganin zasu cutar da Ni dayawa ya san ya na shiga haukar da gangan na dauki wani ita ce cikin rumfar nan aikuwa na sauke wa wacce ta sanya min ya ji. Ganin haka suka yi baya na fara bin su duka da duka ina faɗin duka yau sai na cinye ku ba mai kwana a duniya!!
Sai da na tabbatar sun baje na dawo na dauki guntun jarkar ruwan da suka bari na dunga wanke gabana da ruwan ina hawaye har na dan samu nutsuwa na dauki shawuya yana gefe a ya she ga shi jikina duka ya jiki idan na sanya shi dole ya kamu da yaji ko mura ... ....

PG  14
Haka dole na tsaya har kayana su kaɗan sha na ɗan kara shawuya a gefen cikina na kama hanya domin na bar wannan ƙauyen. Saboda ban san me  zasu min gaba ba, gwanda na bar wurin ko zan samu wata mafaka tunda dai na shigo gari na bar daji.

Da wannan tunanin na kama hanya tafiyar kilo mita guda da rabi ta kawo ni wani babban birni wanda ban san sunan shi ba, amma bisa ga dukkan alamu garin na ta'alawa ne ko kuma jama'ar Nijar. Saboda yadda na ke ganin yawancin su kayu kan su a naɗe kamar dai buza ye.

Haka na kutsa cikin garin tare da Bismillah domin neman tsari da ga dukkan sharri.

Kusan magrib na samu wata rumfa a cikin. Wata tasha na fake saboda ban san ina zan nufa ba, sai kuma tsoro ya cika min zuciya, saboda na san halin mutanen da suke rayuwa a cikin tasha yawancin su ba na gari ba ne.

Sai na chan ja shawara na fita na sake nausawa cikin garin ko zan samu mafaka.

Wani gida na hanga ga dukkan a lamu gidan na masu hannu da shuni ne dan haka na shiga ba ko wani ɗar na fara doka sallama cike da sa'a kuwa wata mace kiwon madara da bota ta fito cikin wani tsadadden leshi ta kalle ni ta amsa min. Abinda ya sanya na ji kwarin guiwa shine yadda ta amsa min ɗin ba wata nuna kyama ko kuma rashin son jama'a. Dan haka na fara koro mata ƙudirin da ke zuciyata na son wurin fakewa kafin gobe saboda ina cikin tashin hankali kuma ban san ina ne nan ba, amma dai na san sunan garin mu kuma idan na samu mota har gida zan iya gane wa.

Shiru ta yi wanda har sai da na fara tunanin ko ba zata taimaka min ba ne sai chan kuma tace, "To na ji dukkan bayanin da ki ka min, sai dai yanzu duniya ta lalace ba gaskiya. Amma duk da haka ba zan barki cikin wannan halin ba zan taimake ki, abin da na ke so da ke shine ki sanar min da abin da kike so. Na farko na taimaka miki saboda ke mace ce kuma bana son na ga mace cikin tashin hankali a duk inda ta ke.

Idan kuma kin zo da niyyar wani munafurci ne ko yaudara to Allah ya na ganin ki kuma ya mai da miki kanki .

"Wallahi Hajiya ba zaki sa me ni da ko ɗaya daga ciki ba in sha Allahu.

"To Allah yasa ina saura ranki."
Ta faɗa tana gyara mayafin da yake ka faɗar ta.

Dago da kaina na yi na dubi shawuya cike da tausayawa na sake mai da kallo na gun Hajiya na ce, "Wannan nake son a fara taimaka da riga saboda tunda yazo duniya bai taɓa sanya ko da wando ba ne. Sai kuma idan da abinci ataima kamin da shi saboda wallahi na kai tsawon mako guda ban ci komai ba.

Sai abinda ya samu cikin kariyar Ubangiji na rayu nida wannan yaron da na raɗa nasa suna

shawuya.

Jin kalamai na tuni na ga tausayi ya wanzu a
fuskar ta, ta kuma jin jina min ta ce, " Muje da ga ciki."
Ta faɗa tana mai juyawa na bi bayan ta cike da farin ciki yau ɗaya zan samu nutsuwa a rayuwa ta na ci abinci na zauna wuri ɗaya ba tare da wata fargaba ba, tunda dai na ga a lamun tausayina a wurin ta.

Ciki muka shiga ta kaini wani ɗaki kamar dai dakin sauƙar baƙi wuri ta nuna min na zauna ta fita jim kadan ta dawo da abinci shikafa da miya harda nama ga wani haɗin shayi mai kauri ta ajjiye min.

Ta sake fi cewa ta dawo hannun ta dauke da kayan sawa na wa da kuma na shawuya masu kyawun gaske.

Farin ciki fal zuciyata kamar zanyi ihun murna na durƙuhe a wurin ina hawaye ina godiya .

"Ba komai baiwar Allah ki ci abinci ."
Ta faɗa ta na fita a ɗakin .

Ai kuwa ban yi ƙasa a guiwa ba na fara aikawa cikina abinci sai da na ji na yi hani an tukunna na ture gefe guda na dauki kofin shayin da na ɗaga sai da na shanye na sauke, wata zufa ta ke sai na yi hamdala ga Allah .

Mai makon na sanyawa shawuya kaya sai na mance da wannan batun kawai na hau kallon sa ina masa waƙa abinka da uwa da ɗa.

Shikuwa ƙuru ya yi yana kallona domin ko dariya bai fara ba, idan yana yi ma ban sani ba tunda ban taɓa samun nutsuwa ba sai yau.

Har wajen minti talatin tukunna Hajiya ta shigo ta dube Ni ta ce, "Ga bayi nan cikin ɗakin kiyi wanka kiyi ma yaron ki shi ma sai ku sanya kaya ."

Da to na amsa mata ta fita na ta shi na shiga cikin bayin na ga komai yadda yake na san kan abin tunda dai ni ma y'ar zamani ce kuma wayayya ƙaddara ce ta mai dani haka! Ruwan zafi na haɗa na sanya shawuya na masa wanka tas bawan Allah yana ta kallo na shidai na ajjiye shi gefe guda nima na fesa wanka harda su gasa jiki. Na sake dauraye shi fes muka fito zuwa ɗakin kayan na sanya shi ma na saka masa na shi.

Ba laifi mun ɗan farfaɗo sosai sai dai uwar rama a gareni kam ba magana, saboda kallo ɗaya zaka min ka ɗauke kai !

Tuni na ji wani irin bacci mai nauyi ya kamani dan haka sai na kwanta kamar wani gida na samu ba wata fargaba, aikuwa bacci ya ce salamu alaikum.Na jima ina bacci tukunna na farka na ga Hajiya zaune kusa da ni ta yi min murmushin.

Na ce "Dan Allah kiyi haƙuri wallahi ban san baccin yazo min ba."

"Kai haba dai ai shi bacci baya sallama karki damu. Yanzu kina a jahar Nijar ne kuma cikin garin zinder. "

Idanu na zaro ta re da furta, "zinder!!"

"Tabbas kuwa."
Ta bani amsa.

"Hajiya ji na yi abun ya yi nisa nifa y'ar jahar Yobe ce kuma a ƙaramar hukumar  kanamma.

"Chab! Gaskiya kina ne sa. Amma me ya kawo ki nan? Kuma me yasa kika faɗa cikin wannan halin?

Shiru na yi kamar ba zan ce komai ba, saboda ban son na tuna koda tsinke ne a cikin labarin a binda ya faru da ni amma ya zama dole na sanar mata halin da na ke ciki.

Dan haka na tsunduma ƙogin mummunan labari na farko har zuwa yanzu.

Banyi mamaki ba ganin fuskarta sharkaf da hawaye, saboda na san labari na ya chan chanci a yi masa kuka.
Saboda na fuskanci ƙalubalen da ni kaina ban taɓa tunani ba.

Ta tausaya min matuka sosai yadda kukasan y'ar uwar ta ta jini.
Cewa ta yi da ni, " Ki kwantar da hankalin ki in sha Allahu idan mijina ya shigo gida anjima zamuyi magana, kuma zaki koma gida da yardar Ubangiji."

Na yi farin ciki mara misaltuwa sosai da sosai dan banyi tsammani samun haka daga gare ta ba.

Amma kuma babu abinda ya fi ɗaure min kai kamar yadda na ji wayar da Alhaji mijin Hajiya ya ke yi da dare bayan ya shigo gida........

Wani irin yawu na haɗiye da na ji batun nasa saboda na san ko shakka ya ganni ko ya ji labari na to tabbas nida shawuya gudun mu ya zama na banza! Tunda abinda ya ke nema ne ya samu har gida.

Kamar na gudu idan na tuna da irin wayar da yake yi saboda kalaman sa babu Allah a ciki

Tunda na ji yana cewa ina zai samu mace mai ɗayen jego ya haiƙe mata kuma sanan ya bada jinta tunda ba zai iya bayar da matar sa ba!

Ban san me suka ce masa ba dai na ji ya sake ce mu su zai duba lamarin.

Kuma na san tabbas yau Hajiya zata sanar da shi zuwana. Abin da zai ji kawa shine kaya ya tsinke a gindin kaba!

Ni kadai na ke ta batun da ba ni da mafita. Shin ko sulalewa zanyi na gudu ne a cikin daren yau? To idan na gudu kuma me Hajiya zata fassara Ni?

Idan kuma na zauna har garin Allah ya waye to tabbas na san Alhaji zai so ya ganni!

Da wannan tunani dai na ke zaune har na fara jin ya kamata na sanar da mahallici na domin shine komai na wa a duniya ta da kuma lahira ta.

Alwala na yi na hau darduma na fara karatun Alkur'ani cikin ƙasa da murya tunda dai ina da sauka a kaina dan haka na yi ta karatu har zuwa wani lokaci da bacci ya fara cin ƙarfina, addu'o'in ne man tsari na yi na sanya sakata a ɗakin domin ji na ke cikin dare ma Alhaji zai iya zuwa ya same Ni dan haka sai da na sa sakata na kwanta.

Basma ce ta ke ta faman tafiya bakin titi hannun ta dauke da manyan ledoji na kayan ɗanyen da ta siyo a kasuwa hannun ta ɗaya kuma rike da hannun yarima har sun zo zasu gifta wata mota ta jam'ian tsaro ta ji yarima ya kwace hannun sa daga na ta motar ya nufa da gudun sa ya sha gabansu wanda tilas direban motar ya ja wani wawan burki! Ganin abinda yarima ya aikata tuni ta shiga damuwa saboda da sun buge shi ya zatayi ? Kuma ta san halin sojojin nan da masifa shin yanzu wanne hukunci zasu ɗauka a kanta tunda zasu ganshi ƙarami ne ƙila suce ita ta ce ta sanya shi .

Tuni wani soja ya duro daga saman motar ta su ya tun kare shi, kafin ya yi magana yarima ya fara magana kamar haka,. "Yawwa zo ka kashe ni tunda ko ina kuna nan kuna yawo amma kun ƙi karɓo min mommy daga hannu y'an ta'addan da suka sace ta! Ka kashe ni don Allah na huta da wannan damuwar! Kashe ni ko zan dai na tuna halin da mommy ta ke ciki. Bana son rayuwa! Na ce bana son rayuwa!!

Ya faɗa cikin amo mai sauti! Wanda dukkan wanda ya ke kusa sai ya juya.

Ga baki ɗayan su sojojin sai da suka tsaya suna kallon yarima, ni kuwa ƙamewa na yi da tunanin irin hukuncin da yaron zai jamin.

Amma cikin iko na Ubangiji sai na ga ɗaya daga cikin sojojin ya zo kusa da shi ya durƙusa ya rungume shi ya na hawaye.

Cike da mamaki na saki ledar kayan hannun na suka zube ƙasa saboda ban taɓa ganin soja yana kuka ba. Kuma ance suna da taurin zuciya ba sa kuka da wuri.

Amma kuma sai ga akasin haka a wurin wannan sojan.

Ya ce "Yarona ka yi hakuri mommy zata dawo gida ka ji, ka tuna min yadda na rabu da uwata amma ban samu ko ganin gawarta ba. Haƙika uwa uwa ce, idan har wannan yaron zai damu da uwar sa to tabbas uwa ba abin ya da wa ba ce. Haƙika na tausayawa wannan yaron saboda yana cikin maraicin uwa, kuma wallahi da da yadda zanyi a yau sai na je na dawo da mahaifiyar sa. Amma sai dai kash! Nima umarni na ke bi.

Ya faɗa yana ƙarewa sauran sojojin kallo .

Wani daga cikin sojojin ya ce ina wacce kuke tare? Ko kai kaɗai ne?

Wata irin faɗuwar gaba ta riske ni saboda na san dole sai sun min tsawa kuma ban kaunar ko da kallon soja ne a rayuwata bare magana da shi.

Dan haka yarima yana nuna ni na fara mazari ina ƙifta idanuna.

Kalaman sojan ne suka daki masarrafin da ke kai min sauti, wani yana yi na ji gaba ɗaya ya riski zuciyata saboda ba haka ka tsammachi muryar ba.

Dan na zaci zan ji ta kamar sauƙar aradu ne.. amma kuma sai na ji ta cike da sanyi da nishaɗi wanda har sai da na lumshe idanuna na bude.

Ganin ban ce komai ba wani daga sama ya rattaɓa min tsawar da sai da na take ledar kayan miyan.

Da in ina na fara magana, "Don Allah kuyi hakuri yana cikin damuwa ne wallahi bani na sanya shi ba. Kuyi hakuri."

Murmushin na ƙasan ya yi ya ce "Ka ma shi ku tafi ki sanar min da gidan ku an jima zan so wurin baban sa idan yana nan."

Sanar masa na yi cike da fargabar abinda zayyi na kama hannun yarima na su ri kayan miyan na yi gaba ba ko wai wa ye.Sauri na ɗinga yi har muka dawo gida.

Koda mama ya Fido ta ganni cikin wannan halin ta san akwai abin da ya faru, dan haka duka suka tsare ni da tambaya.

Banyi ƙasa a guiwa ba na sanar musu komai da ya faru.

Kowa ya yi mamaki a kan abinda yarima ya aikata.

Dan haka Hadiza ta kama hannun su ta ce  "Karka sa ke wasa da rayuwar ka da sun buge ka fa? Bana son irin haka.

Shi kuwa faruk kasa cewa uffan ya yi har sai da aka ce wani soja yana magana a bakin ƙofa tukuna ya yunƙura ya fita saboda baba baya nan dole shine zai wakilci gidan .

Koda gari ya waye kubra ta kasa samun sukuni, jin an taɓa kofar ba ƙaramin tashin hankali ta shiga ba da ƙyar ta samu ta buɗe.

Ganin Hajiya dauke da manyan fulasai na abin ƙaryawa ya sa dole na ƙirkiri murmushin dole tare da russunawa na gaida ta .

Amsawa ta yi cikin sakin fuska ta kuma sanar min da na ci abinci zata zo muyi magana anjima idan na gama.

Ko da ta fita sam na kasa sanya abinci a bakina saboda sai na ji kamar an sanya min wani abu acik. Amma idan na tuna da halin kirki irin na Hajiya sai na ji kawai bazata sanya min komai ba, kuma ƙila bata san ma mijin na ta yana aikata wani mummunan aiki ba.

Da haka na ƙudiri niyyar cin abincin.

A falon Hajiya kuwa Alhaji ne zaune yana waya cikin raɗa yana cewa, "Ranka ya daɗe in sha Allah komai ya zo karshe.......

PG 16
Shigowar Hajiya ya sanya shi ƙatse wayar yana faɗin "Hajiya bari na je na dawo wani lamari ya ta so min da wuri."

"To Alhaji kuma na ce maka muna da baƙuwa mai neman taimako amma da ka tsaya ka ganta ai."

"Kash! Hajiya ina ce  a gidan zan kwana? Maganar nan abarta idan na dawo ma yi ta."

"Shike nan yadda ka ce, Allah ya dawo da kai lafiya."

Da Amin ya amsa ya na saɓa binjima a ka faɗar sa ya fice.

Cike da damuwa ta zauna a falon saboda ta so ace ya ji batun ta sun taimaki wannan baiwar Allah da ta ke neman taimako.

A ɓangare Kubra kuwa abinci ta ci ta ƙoshi saboda ta miƙiwa Allah lamurran ta duka!

Shigowar Hajiya ne ya sanya ta ta yi zuru tana jiran taji mai zai faru.

Hajiya kuwa zama ta yi gefen ta ta ce, "Kubra, ina me baki haƙuri saboda Alhaji ya fita cikin gaggawa bai tsaya ya ji batun ki ba, na so ace ya tsaya na sallame ki yau kin ko ma ga ahalin ki.
Sai dai kash! Ya fita tun bai ji ba kuma ba zai dawo ba sai dare.
Dan haka don Allah kiyi hakuri zuwa gobe sai ki ta fi."

Tunda ta fa ra batun ta na sauƙe wata kyakkyawar ajiyar zuciya saboda na ji akasin abinda na ke tunanin ji.
Ganin ni ta ke saurare sai na yunƙura na buɗe baki na ce "Hajiya na gode sosai da taimakon da kike min ko na ce ki ke kan yi. Amma idan ba damuwa zan iya ta fiya ba tare da Alhaji ya dawo ba, tunda wallahi iya taimakawa a rayuwa kin taimaka min. Tunda na shiga wannan halin ba wanda ya taimake ni kamar ki."

"Haka ne, ina son ki haɗu da Alhaji ne saboda ki samu ta go mashi mai yawa. Amma idan kina

son tafiya gida sai na kaiki na sanya ki a mota ki tafi.

"Yadda kika ce Hajiya ni mai biyayya ce."

"Na fuskanci kina son zuwa gida kuma daman dole ki so hakan duba da irin yadda kika sha gwagwarmaya.
An jima yarona yarima zai zo sai ya kai mu ta sha."

Jin ta ambaci sunan yarima sai da zuciyata ta doka! Ya Allah na ko yarima ya rayu? Ko ina fullo ta yi da shi? Tuni na ji kamar na yi tsun tsuwa na je gida.

Ganin ban ba ta amsa ba ne ya sa ta ce, "Bari na shiga na shirya kafin ya zo."
Kai na gyada mata a lamun to sai ta wuce cikin part ɗin su na koma cikin sabon tunani.

Koda haidar ya fita ya samu soja tsaye gaisawa sukayi da shi ya ne mi da ya ga na da mahaifin su.

Sai ya sanar masa baya gida amma idan ya dawo zai raka shi wurin sa kawai ya basu layin sa .

Kafin sojan ya yi yunkurin bayar da layin sai ga baba Bala da Nasir ɗin sun dawo .

Ganin soja a wurin sai da zuciyar Nasir ta buga yana fatan ace labari kubra aka zo masa da shi.

Bayan sun bashi wuri ya zauna ya ke sanar musu da dalin zuwan na shi. Yana son ya ji ya abin ya ke daga bakin manya.

Labarin suka ba shi tun daga farko har ƙarshe da kuma abinda fullo ta sanar musu game da Kubra ɗin.

Koda ya ji komai ya yi matukar girgiza sosai Dan haka ya miƙe tsaye yana mai mai ta kalmar innalillahi wa'inna ilaihirrajiun.

Tuni suka shiga halin ɗimuwa suna son sanin me ya ke faruwa.

Kallon su ya yi ya ce baba haƙiƙa mun tafka babban kuskure wallahi . Saboda duk lokacin da

muka gaza haɗuwa dasu to muna shirya musu kwanta bauna ne daga baya.

Ina mai ɓakin cikin sanar muku da ce wa bayan fitar su ba jima wa cikin daji jirgi ya sanya musu wuta duka sun ƙo ne. Kuma bana raba ɗayan biyu matar nan sun dauke ta, dan da basu dauke ta ba da tabbas ta bayyana yanzu.

Nasir jin kalaman sojan ya yi kamar wutar garwashi wanda bai san sanda ya chakumi wuyan sa ba amma kuma ko kalma ɗaya bai furta ba ya fadi ƙasa kamar gawa.........

PG 17

Ganin ya zube ƙasa ya sanya haidar ru gowa da gudu ya sanya hannun sa ya tallafi baban su yana faɗin " Daddy dan Allah ka tashi Karka barmu yadda mommy ta barmu, ƙarya ya ke mommy bata mutu ba. Daddy Please! Ya faɗa cikin wani irin kuka me sauti har sai da jama'ar gidan suka fito.
Baba Bala kuwa ya ka sa komai jikin sa sai mazari ya ke yana kaiwa da kawo wa, chan tukun na ya ce da sojan, "Bawan Allah me ne ne gaskiyar lamarin maganar nan ta ka."

Soja ya gyara tsayuwar sa tamkar ba shi ya kawo tarzo mar ba.

Ya ce " Baba ina zato fa na ce tunda mun jefa musu wuta kuma sun ƙone, idan har ta na ciki ka ga ai sai dai hakuri amma idan bata ciki to ƙila tana wurin su a raye ko wani wajen."

Baba ya yi shiru na wani lokaci Sannan ya ce, "Shike nan mun gode da ziyara Allah ya sa tana raye."

"Amin baba. Amma ba shi kaɗai ya kawo ni ba idan ba damuwa ina son ganin yayar yarima saboda akwai wata tambaya da zan mata ."

Badan dai soja ba ne da ba abinda zai hana baba Bala yi masa rashin daraja, amma ba yadda zayyi tilas ya haɗa shi da basma ya yi da daidai da lokacin da Nasir ya farfaɗo da ga sumar da ya yi. Sannu suka fara masa suka shiga da shi gida saboda har jama'a sun fara taruwa.

Basma kuwa ƙuru ta yi gaban soja tana jiran me zai ce mata.

"Ina son ki bani lambar wayar ki ko wata lambar da zan sa me ki. Saboda akwai wasu bayanai da na ke nema a wurin ki amma yanzu na ga baki da nutsuwa sosai."

Shiru ta yi na wani lokaci dan harga Allah ta ji haushi da ya tsayar da ita a wannan lokacin da suke cikin damuwa, kuma shine silar komai da ya faru a  yanzu."

Lambar ta ambato masa ya sanya cikin wayar sa ya yi gaba ta shige gida.

Koda suka shiga jajan ta lamarin suka yi ya yinda mama ta kama kuka wiwi wai tunda yace haka ta san zayyi wuya a ce Kubra na ra ye.

Haka su ka yi ta lalla shin ta har ta ɗan tsa gai ta.

Kubra zaune tana jiran zuwan Hajiya da yarima domin su Kaita ta sha, shawuya ta dauka ta fara masa waƙa kamar haka.

Shawuya bawan Allah ne.

Shawuya ɗan gatan mama.

Allah ya so mu da nisan kwana yarona.

Zamu gida ka ga daddy da sauran yayye yarona.

Dariya ya ɗan ɓangala ai kuwa kubra ta yi da murna yau yaron ta ya yi dariya.

Lamari kamar wanda a kansa ne ta fara haihuwa.

Wajen sha biyu hajiya ta shigo ta ce ta zo su tafi dan haka da murna ta fito ta dauki shawuya ta goya a bayan ta. Kayan da ta cire daman ta daure a leda dan bata son rabuwa da su ko dan tarihi.

Suka kama hanyar fita zuwa gun motar yarima .

Tunda ta ga kallon da yarima ya ke mata sai ta ji hantar cikin ta ta ƙada saboda na kasa fassara ya nayin  kallon na sa.  Har mun shiga Mota da Hajiya sai na ji ya ce. "Dear, ai ba sai kinje ba kawai zan kaita. Saboda ta chan zan wuce sch ne."

Wani abu na ji ya chaki zuciyata kamar na yi ihu tun ban san me Hajiya zata ce ba.

"Yanzu kana nufin na sauƙa zaka yi koma yadda ya kamata?"

Tabbas kuwa dear zan kai ta mana badai Yobe zata je ba? zan sa ka ta motar difa daga nan sai su kaita maini ko kuma ta shiga ta garin su darect kawai ."

"To yarima amma dan Allah kayi wa direba bayani sosai kar ya barta ta sha wuya  ya yi ƙokari ya sanya ta motar garin su da wuri da su ke difan."

"Ok Dear."

Kallon su na tsaya yi na ke kallon Hajiya. Kamar ta san ina cikin ta shin hankali ta ce, "ki kwantar da hankalin ki wannan zaiyyi komai kamar ina nan kuma in sha Allahu zaki je gida a yau ba sai gobe ba.

Ba dan ma ba ƙasa ɗaya muke ba ta kin sanar da zuwan ki a wayar jama'ar gidan ku.

Amma ga wannan ta faɗa ta na bani wasu ƙudi wanda zasu kai naira dubu ishirin. Hannu na sanya na karba ina godiya ta re da share wata ƙwallar da ban san da zuwan ta ba sai ɗumin ta da na ji kan fuskata.

Fita ta yi ta na ɗaga mana hannu har muka ɓace wa ganin ta .  Kallo na na kai kan shawuya na sha kansa a cikin zuciyata na ce "Allah ya raya min kai ya kaimu gida lafiya shawuya.

Jin sautin yana waya ne ya sanya ne ɗagowa da kaina domin na ji mai zai ce,

Kalmar da ya ambata ita ce ta yi sanadin daukewar lumfashina na wucin gaɗi. Bayan wani lokaci na samu damar hadiye wani mugun ya wu hannu na daura bisa kaina na furta " Na shiga uku! Ya Salam! Haba dan Allah wannan wacce irin masifa ce..... Wawan birkin da yaci ne ya sanya ni sake tabbatar da batun da na ji ya na yi ya zama gaskiya..

Shike nan nikam na shiga uku ina jin har abada bazan koma ga ahalina ba.......

PG 18

ganin yan ƙokarin chusa kan motar cikin wani wawa ke ken gida tuni na tuna da maganar da ya yi a waya.

*Daddy ba wata matsala ga ta na kawo ta*
 Wani hawaye na ji suna zubomin ya yinda ya yi dai dai da tsayuwar motar cikin rumfar ajjiyar motocin gidan.

Fitowa ya yi ya bude inda na ke ya ce na fito fuska ba walwala.
Ba yadda zanyi haka dole na sa ƙafa na fito riƙe da shawuya a hannuna. "Bi yo ni .". Ita ce kalmar da ya furta min wanda ta daki dukkan sassan jikina.  Haka na dunga binsa a baya har muka kai ga wasu manyan faluna na gani na faɗa kuma gidan yana da zurfi sosai mun wuce manyan falo sun kai biyar, daga bisani muka bi wani korido muka kurda ta wata ƙaramar hanya muka iske wani ƙaramin falo. Wani jibgegen mutum ne hakim ce a zaune kam wata kujera fuskar sa dauke da murmushi,  idan ka kalle shi ba zaka ce ya yi kala da mugayen mutane ba. Saboda cikar zatin da Allah ya masa kuma ga shi da kwarjini a ido.

Hannu ya miƙawa wanda ya ke zaune tare da faɗin, "Daddy gata nan kuma ba wanda ya ganmu mommy da kanta bata san ma ka ganta ba tunda tana ta mitar rashin tsayuwar ka ."

Dariya ya yi mai sauti sannan ya ce, "Ai shine da lilin da ya sa na ƙi tsyawar domin bana son ta zargi wani abu ko daga baya amma kaga yanzu komai normal. Kai dai abinda zan ja maka kunne ka tabbatar ka sake riƙe mana sirrin mu har zuwa lokacin da zamu fita cikin wannan masifar."

Da to ya amsa masa ya fita ya barni zaune .

Duk jikina ya mutu na kasa ko da kwakkwaran motsi ne ga shi ruwan hawayena ya kasa dai na zuba, sanadin magan-ganun su.
Na sallama wa rayuwa yau kam tabbas amma ma fi tausayin yaro na da zai kai shi gida ni ya kashe da zan amince. Amma sai dai kash na san hakan bazata samu ba, damuwa ta ɗaya ce, ko shakka babu wannan mutum idan ya haikemin kafin ya kai ga biyan buƙatar sa a wurina zan mutu tabbas! Saboda bani da wani kwaliti jiki duk yunwa da gajiya. Ke nan idan na mutu shawuya zai kai kaɗai a shanye wa jini. Zuciyata tana gama bani amsar ƙarshe na fashe da wani uban kuka wanda zaka dauka duka na ake yi.

Ganin abinda na ke yi ne ya sanya Alhaji yin murmushi ya kalle Ni ya ce, "Sorry da kin bar kukan haka dan ba zai Miki amfani ba kam. Ban so na Miki komai ba amma kuma ya zama dole na yi hakan ko dan ceton rayuwar ahalina. Dan haka kiyi hakuri ki dauki wannan a matsayin ƙaddarar ki."

Yana gama faɗar haka ya mike ya na fadin "Ki huta ga kaji chan da kayan more rayuwa ki ci ki koshi zuwa dare sai mu haɗe."

Saman be ne ya haye abinsa, kallon dinning table ɗin na yi wanda ya ke cike da kayan more rayuwa na dauke kaina, domin ba kaza ba ko ɗawisu a ka ban awannan lokacin ba zan iya ci ba.

Yadda ya barni haka ya dawo ya wuce ni ko motsin kirki banyi ba har wajen Yamma ina zaune

in banda sallah da na yi ita ma da taimama na yi ta saboda a kwai wani lungu kafin mu shigo ɗin na ga ƙasa dan haka chan na je na yi na dawo na yi sallah.

Na shiga tashin hankali matuka ainun ganin dare ya fara kawo kai ga kuma yunwa da ta ke addabar cikina har ta shafi shawuya ya fara kuka saboda bai samun nono mai kyau a wuni yau ɗin ba. Da yanzu ina Chan wurin dangina a na ta murna a na maraba da dawo wata, amma wannan yarima bai kyauta wa mamar sa.

Ya Allah yadda ya ci amanar da maihaifiyar sa ta bashi Allah ka to ni asirin su ka ce ce ko da yaro na ne....na hakura da rayuwar nikam koda na koma gida ba lalle na rayuwa tunda zuciyata ta gama shaƙar bakin ciki na san da wuya na jima bata buga ba.... Na karshe maganar ina kuka mai cin zuciya.

Basma ta na zaune ta ji wayar mama Fido ta na kukan neman taimako dan haka tuni ta dauka saboda ba su cika barin ƙira ba ko za suyi katari da labarin Kubra.

Tana ɗagawa ta fara da Sallama. Shiru ta ji ba amsa kuma daga baya a ka ce, "Basma ce?"
"Eh ni ce wa ye ne?"
Ta mayar da amsa.
"Sojan ki ne." Ya faɗa cikin murmushi.

Wata faɗuwar gaba ce ta riske ta jin ya ambaci kalmar sojan ki ne, ta ya ya zama na ta? Ta tambayi kanta.

"Kina jina kuwa basma?"

"Eh ina jinka soja." Ta faɗa cikin ƙosawa da wayar, saboda haushin ko wanne jami'i ta ke ji da shugabanni, suna ji a na kwashe jama'a basa bin ka du da wuri har sai rayuka sun salwanta.

"Basma ina son idan kin samu nutsuwa muyi wata maga na ne."

Ya faɗa cikin sauti ƙasa ƙasa kamar mai raɗa.

"Ina jin ka ko yaushe zaka iya faɗa saboda bani ba samun tsuwa har sai ranar da aunty Kubra ta dawo gida."

Shiru ya yi na wani lokaci Sannan ya ce , "Karki damu zata dawo in sha Allahu."

"Kai da ka ce ta mutu."

Ta jefa masa tambayar.

"Ina tsammani fa na ce basma." Ya faɗa cikin sanyin murya har sai da ya sa ta ɗan dara
Jin sautin darawar ta ta ne ya sanya shi yin murmushi ya ce "Shike nan ki huta zuwa wani lokaci zan dawo idan kun samu nutsuwa. Amma ki sani wallahi da na san inda aunty Kubra ta ke to da tabbas zanje na dawo da ita har gida kodan farin cikin ki."

Ajiyar zuciya ta sauƙe tana jinjina masa duk da ta san ƙila da wata manufar ya ke haka, amma zan ba shi lokacin na ji ƙarshen gudun ruwan sa .

Sallama ya yi mata ta ajjiye wayar ta kwanta tana na zarin kalaman sa.

A na shi ɓangaren kuwa yana gama wayar ya saki wani ƙayataccen murmushi har sai dai na ge fen sa ya ɗan taɓa shi ya ce "Ya de Captain Jamil, ko ka faɗa soyayya ne?"

"Hummm! Kamal wallahi ba zan ce komai ba a yanzu amma dai kam na san ina daf da faɗawa cikin soyayya. Sai dai da yake ban saba da yinta ba ko kuma in ce ban taɓa ba har wani tsoro na ke ji ni kadai idan na tuna ta."

Dariya sosai wanda a ka ƙira da kamal ya tuntsure da ita ya da fa ƙa fadar Captain Jamil ya ce.
"To kuma me ne ne abin tsoro? Kai dai akwai wani sauna wato idan ba a filin da ga ba baka da wani kuzari."

"Eh daman na miji ai yaƙi a ka san shi da shi.

Da haka dai kamal ya yi ta tsokanar sa har wani lokaci.

Ganin ba wani sarki sai Allah yasa ta gyara zaman ta amma kuma sai ta tuna cewa ta gwada buya mana ko Allah zai sa ta tsira idan da rabon rayuwar ta zatayi tsayi.

Da wannan tunanin tashige wani lungu wanda ba lalle a san da mutun ba a ciki.
Dan haka da Alhaji ya dawo ya sha mamakin rashin ganin ta awurin. Amma ko kaɗan baiyyi tsammanin zata buya ba ko ta gudu tunda dai ya san gidan nan daga shi sai a halin sa suka san kan gidan.

Amma wani abun mamaki duk yadda ya ne mi ya ganta ya rasata, har ya fara haɗe gumi yana ƙiran ke baiwar Allah wallahi kiyiwa kanki ƙiyamar laili ki fito tun kafin na kamaki!
Amma shiru. Iya ta shin hankali ya shiga a wannan lokaci dan haka ya ƙira yarima ya ke sanar

masa ko dai yazo ya tafi da ita ne. Amma yarima ya ce sam bai dawo ba ya dai sake dubawa tunda dai bawan da ya ke iya shiga gidan sai shi sai Hajiya su suka san password ɗin gidan .

Abin mamaki dai Alhaji ya rasa kubra kuma ya gaza tafiya gida daman shirin sa shine idan ya biya bukatar sa da ita sai ya wuce gida da sa fe ya kaita wurin oga! Amma kuma ga shi ta kwafsa masa. Saboda haka ba yadda za'ayi yabar gidan har sai ya ganta koda zuwa gobe ne tunda dai ya san ta na gidan .

Wayoyin sa ya kulle duka saboda kar wani ya kira shi ma data gidan sa.

Hajiya kuwa iya tashin hankali ta shiga na rashin dawowarsa gida ga wayoyin sa duka ba sa shiga.
Ta damu yarima da yaje ya duba ko yana dayan gidan amma sam ya ce ba wani abu sun yi waya ya ce aiki ne ya masa yawa. Dan haka dole ta koma part ɗin ta.

Shi kuwa ya faɗa mata haka ne dan ta barshi tunda dai ya san inda daddy ya ke amma dai bai dauka zayyi amfani da ita ba ne iya abin da ya sani zai kaita wajen oga ne a maimakon Hajiya da suka so a abasu wanda tsautsayi ya jefa daddyn su ciki kuma yana addu'a ya rabu da su lafiya kafin su cutar masa da mommyn sa.

Gari na waye wa Hajiya bata yiwa yarima magana ba ta fice kai tsaye gidan Alhaji ɗayan ta na zuwa ta sanya hannu ta bude  ta shiga.

Shi kuwa yana cikin falon abin duniya ya masa yawa dai yau yayi da na sanin rashin sanya cct Camera  a wannan ɓangaren. Kuma ya yi haka ne saboda ko da wani abu zai faru irin haka wataran kar Hajiya ta je ta kallah kuma dai gashi yau da yana nan da ya masa rana .

Jin sautin shigowar mutun ne ya sanya shi ɗagowa cikin firgita sai kuwa ya yi arba da Hajiya, tuni ya miƙe ya fara in ina yana mata sambatu na karya. "Wallahi ina cikin damuwa ne ban son koma wa gida ki shiga ta shin hankali."

"Haba Alhaji ko wacce irin damuwa ce ai gwanda ka dawo gida ka kwana kusa dani....."

Jin sautin Hajiya ya sanya kubra ta miƙe da ga buyar da ta yi dan dole ta fita dan idan Hajiya ta ganta tabbas zata samu fita daga wannan gidan. Tunda daman ta galabaita ga kuma yunwa ga shawuya suman sa biyu kafin waye War gari bata san mai ya dame shi ba ga shi ko kuka bayyi ba bata san me ne ne matsalar sa ba. Dan haka fitar ita ce mafita kawai

Alhaji yana yiwa Hajiya daɗin baki kawai sai ji ya yi kubra tana faɗin .

"Hajiya ki taimake ni wallahi zai kashe Ni ......!" Cike da ɗimuwa hajiya ta juya ta dube ta cikin tsantsar mamaki ta ce "Kubra! Wa ya kawo ki nan "

Bata samu damar magana ba saboda Alhaji ne ya yi zaraf ya ce .

"Gwanda da kika bayyana kanki matsiya ciya! Ai yanzu kin gani tsintacciyar mage........ Halin ki na taimakawa al'umma ya ja ana neman raba ki da mijin ki, ya faɗa yana goge ido tsabar iya munafurci..

Ta shin hankali ne ya ziyarci zuciyar Hajiya gaba-daya ta ka sa gane inda ya dosa .... Ita kuwa kubra ka sa koda motsin kirki ta yi.........

PG 19
Ganin irin sharrin da Alhaji ya ke neman yi mata ne ya sanya ta dur ƙushewa a wurin da take.

Hajiya ta kalle ta ta sake maida kallon ta a wurin Alhaji ta ce "Me ya haɗa ka da Kubra? Wa ya kawo ta nan? "
Ta jera masa duka tambayoyin.

Sanin cewa Hajiya mace ce mai kishi Dan haka tuni ya shirya irin ƙaryar da zai mata.

"Ban san ya akayi ta zo ba, kuma abinda ya ban mamaki shine yadda ta hanani ta fiya gare ki jiya ban san irin ƙarfin asirin ta ba."

Ya faɗa cikin muryar kuka wacce tuni Hajiya ta ruɗe duka tunanin ta ka sa gane mata wannan shiryayyiyar magana ce, wanda dukkan mai hankali ya kamata ya gane ƙarya ce domin idan ba rami mai ya kawo rami? Amma saboda tsantsar kishi irin na Hajiya ga shi ta ji ya ambaci asiri da son rabashi da shi ai bata yi wani tunani ba ta nufi kubra cikin damuwa, ita kuwa Kubra bata ce da ita komai ba saboda ya riga da ya ɗaure ta da jijjiyar jikintaTa na zuwa wurin kubra bata ɓata lokaci ba ta wanke ta da mari hagu da dama.
Wanda ya sanya kubra zubar wasu hawaye Masu zafi, amma kuma bata da bakin magana. Hajiya ta fara mata masifa, "Lalle tsintacciyar mage bata mage! Ni kubra! Ni zakiwa haka? Duka alherin da na miki, da kar ɓar da na miki na baki wurin kwana sutura abinci! Duka da abinda zaki saka min ke nan."

Jin kalaman ta duka sai suka sanyawa zuciyata damuwa na ji kamar da gaske na aikata mata laifi, cikin ƙarfin hali na bude baki na fara mata magana cikin dusa shewar murya.
"Hajiya dan Allah ina son ki saurare ni, bazan yi ƙoƙarin ka re kaina ba a gare ki domin ba lalle ne ki fahimta ba. Amma sai dai yadda na same ki mai taimako na ji matukar baƙin ciki da

kika kasan ce mai watsar da ladan ki tun ba ayi nisa ba. Dukkan wanda ya yi abu domin Allah koda anbi shi da sharri ba zayyi go ri ba. Idan har domin Allah a kayi , amma duk da haka ina roƙon Allah da ya bar miki ladan ki, saboda tunda na faɗa halin da na shiga ba wanda ya min abinda kika min na alheri kamar ki.
Dama mu mata muna da wannan raunin duk yadda muka kasan ce da saurin tausayi amma ba mu da wuyar zubar da ladan sai mu fara da ba gori ba.

Amma ina roƙon ki dan girman Allah taimakon na karshe da zakiyi min ki fitar da ni cikin gidannan, sannan ki tuhumi mai gidan ki domin bai kamata yadda kike da hali na gari kin zaune da wanda baki san ko waye ba."

Na karashe maganar cikin kuka ina zuƙe majinar wahala.
Tunda na fara magana Hajiya bata ce komai ba kuma duk jikin ta ya mutu da magan ganu na dan haka shiru ta yi tana nazarin kalamai na. Ganin haka ya sanya Alhaji zabura min da cewa.

"Muna fuka wato har kina da bakin wa'azi? Ke ce fa kika zo da kanki har kina cewa a nuna miki hanya? Ai daga nan sai gidan gyran hali."
Hajiya wuce muje idan munje Chan ta faɗa Miki yadda ta shigo .

Ita dai Hajiya kasa magana ta yi, har sai da ta jinjina lamarin a zuciyar ta sannan ta ce , "Ko ma me ne ne yanzu ta bar mana gida bana son sake ganin ta bare ma mu yi zaman shari'ar har ta samu damar rabani da kai ɗin. Dan haka kawai yanzu ta bar gidan! Ta faɗa cikin faɗa da masifa .
Ganin haka Alhaji ya yi kanta ya fara faɗin "To muna fuka a yi gaba maza yallah ! Allah ya so ki da kin shiga uku! "
Ita kuwa kubra ba ƙaramin daɗin ta ji ba da jin kalaman Hajiya dan haka ta goya shawuya ta fara shirin ta fiya sai dai kuma kash! Bata san hanyaa ba . Ganin ta tsaya ne Hajiya ta du be ta ta ce "Me kike jira kuma."
"Hajiya wallahi ban san hanya ba ."

Hajiya ta juya ta kalli Alhaji, kafin ta yi magana ya yi zuruf ya ce, "Hajiya ba zaki fita hanyar munafukar nan ba wai ?"
Kallon sa ta yi har sai da ya tsargu da kallon da ta ke masa sannan ta ce da kubra bi yo ni.
Ta yi gaba kubra ta bi bayanta ta na hamdala a zuciyar ta. Har bakin ƙofar gidan ta raka ta tace, "Allah ya ki ya ye hanya Allah ya rabani da ke har abada! Idan ma kina da gaskiya ke ta sha fa ! Idan ma baki da na barki da Allah."

Duk kalaman ta sun fa ɗa cikin zuciyata na ce da ita ba tare da ja juya ba. "Allah ya biya ki da gidan aljanna."

Na wuce na kama hanyar wani babban titi da ba abin hawa da yawa kasan cewar birnin Nijar daman bai cika cin ƙo so da yawa kamar irin su Kano ba, tafiya mai nisa na yi na tare mai abin hawa na ce ya kaini tashar difa. Kai tsaye ya dauki hanya ya kaini ina zuwa tasha kuwa na

samu mota mutun guda ya rage dan haka na afka cikin farin ciki. Hanya muka ɗauka ina hamdala Allah ya kaimu lafiya.

Ta fiya muke cike da kwanciyar hankali amma Ni kuwa bani da wani burin da ya wuce a ce na ganni gida. Dan gaba daya zuciyata sai bugawa ta ke ban san dalili ba! Amma kuma sai na ga wani mutum mai siffar buzaye ya kalli na kusa da shi sunyi murmushi. Nidai na ce Allah ya fi ku idan ma wani abu ne .....

PG 20

Har mun kusa kai wa maini kawai muka ji wani hayaki ya tur nuƙe mu.
Kowa ya kama tari, shawuya kuwa har da suma tuni direba ya tsaida motar dan haka kowa ya fita .

Amma mai zai faru! Kawai wadanna mutane guda biyu suka cire wasu manyan wuƙake suka ce kowa ya bada kudi ko kuma wani kayan kuɗi, amma kaf ɗin mu suka ce ba kudi a jikin su, dan haka nima daman kudin nawa yana cikin dan kan faina ban masa ruƙo na wasa ba saboda na san zai min amfani.
Ganin zamu ɓata musu lokacin ne yasa ɗaya daga cikin su ya fizge shawuya ya ɗaura masa wuƙa a wuya ya ce kowa ya fito da kudin jikin sa ko kuma mu yanka yaron nan a gaban ku kuma kuma mu yanka ku. Ganin haka tuni na tsare har lumfashina yana sarƙewa na saka hannu cikin jikina na cire duka kudin da Hajiya ta bani na bashi ina karkarwa, dariyar mugunta ya yi sosai ya ce, "Allah ya so ki munafuka karɓi ɗanki!"
Ai kuwa hannu yana rawa na karbi shawuya ya yin da kowa ya cire abin da ya ke jikin sa ya mika masu. Abu guda ne ya bani haushi yadda mutum biyu rak suka tsare duka motar saboda wuƙar da ta ke hannun su .

Kuma yawancin motar maza ne masu yawa amma saboda tsoran mutuwa ba wanda ya yi wani yunƙurin ceton mu! Bayan mutuwa dole ce idan lokacin ya cika ba makawa sai an mutu ɗin, to amma kowa tsoran ta ya ke .
Idan ba haka ba ai Sarkin yawa ya fi Sarkin ƙarfi, a tunani na mai bindiga shine abin tsoro tunda zai iya harbin ka! Amma mai wuƙa za'a iya cin masu ta dabara idan an so yin hakan.

Ganin na shagala da tunani wata da ke kusa da ni ta ce min " kiyi hakuri kin tsorata ko? Sun gudu fa muje mu shiga mota."

Ban ce komai ba muka dauki hanya kai tsaye direba bai tsaya da mu ko ina ba sai gaidam.
Sauka kowa ya yi ya fara kama hanyar gidan su masu shiga motar wucewa suna shiga amma Ni kuma bani da ko biyar da zan shiga motar kananma.

Sai na yi tunani na je wani gida kawai na nemi aron waya tunda dai ban mance lambar wayar

mijina ba sai na kira shi na sanar da shi ina gaidam tunda ba nisa ya zo ya tafi dani.

Dan haka na yan ke shawarar shiga gidajen da suke bayan ta shar maini domin na ga ko zan samu wayar.

Amma kowanne gida na je ma na lura kamar gudu na suke kawai sai na mike da ta fiya saboda mun taɓa zuwa gaidam so ɗaya da wata makwafciyar mu na ra kota suna amma kuma gidan yana chan a ƙarshen gari ne.
Sai na fara gwada tafiya ko Allah zai sa na gane gidan duk da cewa na san akwai nisa tsakanin tashar maini da anguwar kudu a kwai nisa gaskiya. To amma ba yanda zanyi nan ne kaɗai zanje na samu wayar ƙiran.

Duk da kasancewar gaidam gari ne da kowa ya san shi da girmama baƙo da bashi kulawa amma yau na ga saɓanin haka a gare su, ina tafe ina mamakin chanjawar ta su.
Ashe dai na tarar da su suna cikin ruɗin shaidan ne domin kuwa zuwana unguwar na tarar gidan a kulle ba ko a lamun mutum yana rayuwa acikin sa wata ce ta sanar min da ai ta yi balaguro.
Tsawan lokacin na dauka ina tunanin mafita sai na ji ana kiran sallar la'asar ga yunwa ga ba kudi dan haka na yanke shawara nai man taimakon abinci,  wani gida da naga yara suna wasa. Koda zuwa kofar gidan kawai  yaran suka watse suna gudu suna faɗin kar mu je ta kwashe mana.

Mamaki ya sa na kalle su na ce ikon Allah wato har yanzu ban dawo kamar mutane ba ke nan tunda yara ma suna guduna!
Wata maina na samu na zauna na kira wani yaro da yazo wucewa na sanya shi ya karɓomin ruwa a wani gida na yi alwala na yi sallar azahar da la'asar sannan kuma na ce dan Allah ya maida butar ya ce su aramin wayar su zanyi ƙira .

Cike da sa'a sai ga matar ta fito ita da yaron ta ke ce masa ya bani wayar amma ya yi a hankali kar na kwashe masa dan ita tsoro na take . Mamaki ya kama zuciyata fal, har sai da raina ya sosu duk da cewa na san yadda na ke a bushe dole ne na chanja kama.

Amma kuma bai kamata ana guduna ba tunda dai lalura ce.
Yaro yana bani waya naga ya buga tsalle ya min gwalo, sai matar ta ce masa lafiya kuwa? Aikuwa yaro yana jin haka sai ya fasa ihu ya fara faɗin ta kwashe min su! Mamaki fal zuciyata na ce yau zan ga ikon Allah.
Kafin na ce wani abu wuri ya cika makil da jama'a an fara narko min manyan zagi.
Wayar suka warche suna ja da baya maza suna cukume wandon su mata kuma suna rungume ƙirgin su, na ce " Ikon Allah ! To nidai gaskiya abin da fari dariya ya bani har sai da na dara na ce wai lafiya kuke kuwa.

Ai kuwa wata tana jin abin da na ce ta ce "Zaki ci ubaki yau kuwa idan baki dawo masa da kayan sa ba."

Na ce, "Wai wana kaya ne haka bayin Allah ni fa baƙuwa ce wata na zo nema ban sa me ta ba."

"Yawwa munafuka daman ai baƙin ne suke haka dan dai mu kam kaf! Garin nan ba mai wannan halin! Aha! A mayar masa kayan sa."

Mamaki ya sake lunke min zuciya na haɗiye wani miyau mai shegen zafi na ce,

"Na ce yanzu kun duba kayan na shi ne kunga babu?"

Duka suka yi kaina suna faɗin ba za'a duba ba ba ɗin kalan ki haɗa da sauran ko to ki yi maza ki maida masi
Wata cikin su ta sa ke cewa, kuma idan zaki mai da mushi ki maida mishi na shi! Sai ku dau abin mutum na yaro ku sanya masa na babba, shekaran jiya ma haka wata ta yi a chan layin.

Haka suka dinga jifana da miyagun kalamai har ta kai ga sun fara duka na tukunna wata babba cikin su tace su daina duka na kar su ƙarasa gawar da ba ta su ba garin ne man gira a rasa idanu.

Dan haka sai na samu rangwame aka ne mo mai nafef aka tusa kai na ciki na ji suna cewa aje gidan kangar! Chab ! Duk da ban san ina ne ba amma ina jin makwafciyar mu tana bada labarin wani wurin horo ne da ake kai mai laifi duk girman sa a bashi kashi.
To ni ba wannan ne damuwa ta ba, a'a ta ya ya zan maida abin da ban dauƙa ba tunda na san shine abinda za'a tuhume ni da shi.Muna zuwa gidan kuwa wasu zaratan sojojin suka sakani gaba da tambaya suna cewa ina na kai masa kayan sa, amsa ɗaya na ke bayarwa ita ce " Bansan me suke nufi ba."

Ya sake cewa "Idan baki mayar masa ba wallahi har oga ya dawo daga kananma zaki sha wahala."

Sunkuyar da kaina na yi bance komai ba. Saboda kalmar kananma da yace yasa naji farin ciki, kuma Allah ya kawo ogan ko Allah zai sa ya taimaka min.

Ɗaya a cikin su yace da mai tambaya ta " Wai mutanen garin kanamma duka sun koma ne?"
Amsa ya bashe cewa duka sun koma wanda basu koma ba ma yau zasu koma saboda gobe gwamna zaije ya basu kyauta.

Ni dai shiru na yi bance komai ba har sai da shawuya ya fasa ihu tukunna na tallafo shi.

Sojan ya zura min idanu kamar ya sanni yana ta faman kallona.....
PG 21
Ranar da su basma da su mama fedo Maryam hadiza da su yarima haidar zulfa'u duka suka dawo daga gashu'wa saboda jin labarin sanarwar koma war kowa garin komai ya lafa.
Shi kuma Nasir cewa ya yi suje amma shi kam ba zai koma ba har sai anji labarin kubra. Dan haka duka suka dawo gida ba su zauna ba, suka zo suka tarar garin su ya cika taf da jama'ar garin hamdala suka yi da addu'ar Allah ya sa sun samu zaman lafiya mai ɗaurewa.

Captain Kamal ne ya dubi Captain jamil ya ce, "Wai duk dan basma ta tafi ne ka zama wani salihi ne haka?"

Murmushi ya yi ya ce, "Kai fa baka da kirki wallahi, daman Chan ni salihi ne ai."

"Haka ne kam amma a wurin basma ne ka ke salihin tunda na ga har wani tsoran ta ka ke ji."

"Kai malam ka gane fa ba tsoro ba ne kawai tsntsar love ne."

Dariya sosai kamal ya yi ya dubi Jamil har ya na nuna shi, "To yanzu ina love ɗin? Yarin yar da har ta wuce garin su."

"Wai kana tunanin zan barta ne? Ta turamin hoton yayarta fa, ka ga kuwa duk ranar da Allah ya sa na same ta zan kai mata ita har gida da ga nan sai mu jone."
Ya faɗa yana masa gwalo kamar wasu yara. Sukuma sauran sojojin suna nan suna har ko kin su ba wanda ya sanya musu baki.
Sai Chan wani babba cikin su ya ce "Yau zamu wuce gaidam sai mu jira gwamna da ta wagar sa sai mu wuce kananma."

"Ok sir ba damuwa."

Kallon sa ya maida ga kamal ya ce  "Ka ga rabon haɗuwa ya sa ke faruwa ko."

Kamal ya ce "To gaskiya abokina ina maka fatan alheri domin na tabbata kana ƙaunar yarinyar nan fa, gani ɗaya ka mata ka susuce  har da jin tsoro kamar wani so ko."

Naushi Jamil ya kai masa , "Wallahi baka da kirki ni ne sokon ko? Ba damuwa zan kamaka wataran kai ma ."

"Kai haba ai tsoran mace sai dai kai ɗin amma bani ba kam."

Haka suka yi ta zuba zance har lokacin tafiyar su gaidam ya yi suka dauki hanya .

Ita kuwa kubra ganin irin kallon da yake mata ne ya sanya ta sunkuyar da kanta ƙasa,
Kamar dirar mikiya haka ta ji maganar sa. "Yanzu ke kina da wannan ɗan ƙaramin yaron kike aikata irin wannan laifin haka? Bakya tsoron su cutar miki da yaron ki? Ki mayar musu idan har kin ɗauka musu kayan su kawai dan yau idan OGA ya zo zai wuce zai Miki illah saboda baya barin irin wannan lamarin da sauƙi tunda ya yi fama da irin masu rigimar ki ba sa mayarwa sai dai a gaji abarsu."

Kallon sa na yi kamar ha zan yi magana ba na ce " To taya za su mayar da abinda ba su da masaniya a kai, bayan basu ɗauka ba."

Shiru ya yi ya kalle ni ya jinjina kai irin zaki sani ɗin nan.

Misalin shida na magrib su Jamil suka shigo gaidam suna zuwa kai tsaye bayan sun gaida da y'an bariki gidan kangar ya wuce saboda yana da abokai kuma idan ya je yana yawan samun masu laifi harma ya shiga cikin lamarin ya jibgi masu laifi idan sunyi gardama koda kuwa mace ce bai cika tausaya mata ba. Amma karo guda da ya yi karo da macen da ta wargaza masa lissafi har ma ya ke ɓari akan ta.Suna zuwa  kuwa suka wuce gidan kangar, shigar su ke da wuya ya samu zancen maganar kubra cike da mugunta ya ce kubani ita zanyi maganin ta.

Ana kawota sai da zuciyar sa ta buga  cike da mamaki ya ke kallon ta kamar ya santa, ya sake tambayar laifin ta a ka sanar masa.
  Hannun ya sanya ya ciro wayar sa ya buɗe ma'a danar hotuna kai tsaye kan hoton kubra ya sauƙe idanun sa. Saurin ɗagowa ya yi ya kalle ta ya sake kallon wayar  duk da irin ramar da ta yi amma kamarta bata sauya ba, ya furta, "Kubra."

Cike da mamaki ta ɗago ta kalle shi.  Amswa ta yi cike da mamakin inda yasan sunan ta.

Bata gama mamaki ba ya nuna mata hoton wayar.
Tabbas itace kuwa a acikin wayar.  "Ina ka samu hoto na dan Allah?"
Na jefa masa tambayar.
  Maimakon ya bani amsa sai yace " Ya akayi kika zo nan?"

Ban ɓoye masa komai ba tun daga shiga ta gaidam saboda ina son ya bani amsar tambayar da na masa.

Sannu ya min tare da cewa sauran sojojin da su duba wandon yaron.
  Aikuwa ana buɗe wandon yaro aka sami komai nasa ya na nan .

Dan haka cike da ɓacin rai Jamil ya ce,.  " Wannan abu ƙarya ne fa ruɗun shaiɗan ne kawai, dan matar nan bata da alaka da wannan lamarin.
Kuma mutane suna amfani da ƙaryar yara ne ba tare da sun bincika ba, mutum yazo yana buƙatar taimako amma sai a ɓuge da masa sharri a hau jibgar sa.

Dan haka daga yau munyi watsi da wannan batun.
Kawai yara da sunji ana maganar abu shike nan sai su gwada sai ayi Sa'a jama'a su dauki kururuwar su.

Ba tare da an duba anga babun ba sai dai aga maidowar .

Haka dai ya kashe zancen kuma ya min albishir da gobe in sha Allahu zai kaini har gida .

Murna a wurina har da russunawa na ke ina godiya har na mance batun ina ya sanni nidai kawai na ganin cikin gida.

Gari yana waye wa kuwa gwamna ya iso dan haka muka dauki hanyar kananma ina gaban motar sojoji ram, saboda Jamil ne ya bani wurin sa ya koma baya shi ɗin tsabar yadda hanyar ta ke farkon fita ba titi mai kyau ga yunwar da  ta gama cinye ni ban samu cin komai ba saboda murna, tuni na  fara amai ba kakkautawa har sai da muka je garin gada a ka bani ruwa da doya na gyara bakina na ci kaɗan muka ɗauki hanya sai kanamma cikin farin ciki.

Har wani gashin jikina na ke ji yana kaɗawa yana miƙewa saboda farin ciki na kuɓuta da ga masifa zan dawo rayuwar farin ciki.

PG 22

Shigar mu ke nan na ji wani farin ciki ya mamaye min zuciyata wani haske na ke gani tar acikin na mujiyata yana sake haska min gari.

Na kalli shawuya na manna masa kiss a goshin sa, dan ko ba komai na san tabbas yau zaiga uban sa kuma jinin sa . Farin cikina guda! Idan na tuna duk wannan gwagwarmaya ba wanda ya kutsa kai cikin gonar Nasir, sai na ji kai na har sa ke huruwa ya ke. Domin kuwa na yi wani ƙaramin jahadi ne.

Muna zuwa daidai barikin sojojin muka tsaya nan fa na ga yadda garin ya cika da yawan mutane kowa yana ta har karsa, bani da wani burin da ya wuce na ganni cikin gida.
Amma kuma basu bani damar tafiya ba, kai ni sukayi wurin ogan su domin ya na son ya yi hira dani ko zasu su samu wani ƙarin bayani game da dajin da y'an ta'addan suke rayuwa.
Na yi iya bakin ƙokarina wajen sanar masa iya abin da na sani, dan haka daga nan aka ce

aje dani gwamna ya ganni.

Mamaki fal raina yau nice zanje gaban gwamna ido da ido saboda wani dalili. Haka suka wuce da ni wurin sa ya karɓeni cike da fara'a yana nan nan dani saboda farin ciki.

A chan kuwa tuni jamil ya ƙira basma ya sanar mata ta shirya ya zo kananma kuma yazo mata da wani abun mamaki dan haka yana son kowa ya zama yana gida dan akwai wani batu mai mahimmanci.
Jin haka ya sa aka yiwa Nasir waya maza ya dawo saboda suna tunanin ƙila ya samu wani labari na ne da ya ke son sanar musu.

Dan haka kowa ya hallara suka yi zaman jigun.

Bayan gama tattaunawa ta da gwamna muka ɗunguma zuwa gidan baba bala da kwatancen da basma ta yi masa kasan cewar garin ba shi da wani girma sosai.

Muna zuwa suka ga motar sojoji kusan guda biyar tare da motar gwamna, ai duka sai suka firgita suka fara tunanin ƙila gawata ce suka zo da ita.
Dan haka lokacin da baba Bala ya musu iso cikin gidan kafin a basu bayani har sun fara matsar kwallah.

Nikuwa ina Chan mota ina zaune domin ba su bani damar fita ba.

Jamil ya dubi basma bayan an gaisa da kowa ya ce, "Dan Allah kiyi haƙuri.". Tana jin kalmar haƙurin nan tuni ta rushe da kuka wanda ya yi dai dai sallama ta cikin gidan, duka suka zubamin idanu suka ka sa koda motsin kirki ne.

Yarima ne ya yi ƙarfin halin ta so wa da gudu ya faɗa jikina tare da ta fashewa da kuka yana faɗin, "Mommy na baki mutu ba ashe? Daman zan ganki mommy kafin na zama soja na karɓoki?......."

Ya ƙarahe cikin kuka wanda ya sanya ni nima tuni na fashe da kukan sai kuma dukkan kannena suka taso suka rungume ni suna kukan farin ciki.

Jani sukayi suka zaunar dani suka ƙarbi shawuya suna ta kallon sa suna hawaye ganin yadda jariri da shi amma a lamun ra ma ya bayyana a gare shi.

Koke koke ake ta faman yi kamar gidan mutuwa.
Chan na hango Nasir ya na zaune yana ta kallona yana zubar ƙwallah, hannu na ɗaga masa na masa murmushi kasa jure wa ya yi yazo kusa dani ya ya ƙarbi shawuya a hannun su Maryam ya rungume amma idanun sa ba su fasa zubar ruwan hawaye ba .
Cinyar mama fedo na kwantar da kaina saboda gajiyar hanya, hannu ya sa yana shafin kai .

Gwamna na ne ya yi gyaran murya ya ce ma sha Allah Alhamdulillah tunda ta dawo gida lafiya, sai dai amma fa akwai wata y'ar ƙaramar ƙura da na ke son ku kiyayi bankaɗo ta.......

Dukan mu shi muka zubawa idanu domin muji mai zai ce.........

PG 23

Ganin mun maida hankalin mu gare shi shine ya sa ya ɗan murmusa ya ce, "Karku da mu, ba wata sabuwar matsala ba ce. Abin da na ke son sanar muku shine bana son a yi ta yaɗa dawowar ki saboda wata afkuwar matsalar, ina son a bar zancen anan saboda bazuwar maganar da yaɗuwarta zai sa kuma *bayan gangami* a samu wata ƙura. Ma'anar shine waɗanda kika gujewa zasu iya sake dawowa domin farautar ranki."

Cike da fargaba na ɗaura hannu akai, "Yanzu dukkan wannan wahalar da na sha kuma sai a sa ke biyoni?" Na faɗa cikin muryar kuka.

"Tabbas kuwa! Abu mafi sauƙi shine dole ki sauya wurin zama ki bar wannan garin har zuwa wani lokaci."

Baba Bala ne ya kalle shi ya ce, "Mai girma gwamna taya hakan zai faru bayan nan ne wurin zaman mu?"

"Wannan ba damuwa ba ce ba idan har kun ɗauki shawarar da na baku."

"A'a ai bamu da wata magana sai ta ka mai girma gwamna, yadda ka ce haka za'ayi."

Haka dai suka tattauna suka tsaida magana guda ya ce da baba bala in sha Allahu zai ne mu muyi zama na gaba .

Amma kafin nan ya ajjiye mana bandir ɗin kudi na naira miliyan guda ya ta fi.

Munyi farin ciki da wannan kuɗin ba kaɗan ba, dan haka haka muka wuni a na farin ciki da nishaɗin da koke koke wasu lokuta na murnar dawowar.

Sai wajen magrib tukunna y'an uwa da abokan arziƙi suka sassauta zuwa min jaje da barka da kubuta.

Bayan munyi sallah ne Nasir ya fita ya dawo hannun sa dauƙe da wata leda ya wuce ɗakin su basma ya ce da yarima ya kirawo ni, banyi wani jinkiri ba domin nima na matsu na ke ɓe da shi mu ga na.

Bakin gadon na je na zauna na jingina kaina a ka faɗar sa ya sa hannu biyu ya rungume ni duka a jikin sa ya ce. "Sannu ƙurraty, haƙiƙa mun ga iftila'in da kuma jarrabawar rayuwa. Amma Alhamdulillah yanzu komai ya wuce . Ga wannan ki ci yadda kika sha wuya wallahi idan na kalle ki sai ki na sani kuka idan na ga yadda kika rame gaba ki ɗaya."

Murmushi na yi na kalle shi, "Haka ne kam amma karka sawa ranka damuwa sosai da wannan abinda na ke so da kai shine kawai muyi ta yiwa Allah godiya.

Ya amsa min da kai ya tura min ledar tsire mai ɗumi da lemon ro ba.

Ci na yi kuwa na yi ƙat na sauke numfashi na yi hamdala ga Allah .
Na kalle shi, "Habibi ya kamata na je wurin su mama kar su mana fassara."

Murmushi ya yi sosai har da ɗan darawar sa, "To ƙurraty kije amma ai gobe zamu koma gidan mu tunda yau Zanje na share mana komai dare na gyara."
" Haba kai kuwa dan Allah ka bari gobe su basma suje su gyara sai ku koma kai da haidar kuna kwana amma ni kam sai na yi sati biyu na dawo cikin hayyaci na ."

Baki ya riƙe yana kallona, nikuwa na fice da sauri ban saurari ma wata maganar da zai yi min ba.

Bayan kwana biyu na dan samu sassauci da zuwan masu jaje dan haka Nasir ya zo muka tare ɗakin su basma saboda yau suna makarantar islamiyya, sai mama fedo ce da su zulfa'u yarima da haidar ma suna chan islamiyyar su.

Sani gaba ya yi yace na bashi labarin bayan rabuwa da kuma yadda na samu na kubuta.

Haka na zauna na tankwashe ƙafa na fara bashi labari tunda ga kan rabuwar mu da yarima har zuwa auren da aka ɗauramin, ganin irin kallon da yake min da kuma yadda fuskar sa ta sauya kala idanun sa su ka ƙanƙance ya sanya tilas! Na tsaida labarin ......

PG 24

Kallon sa na yi cike da mamakin irin wannan kishin, saboda ni a tunanina wannan ba lokacin ba ne na nuna kishi ba! A'a lokacin ne na farin ciki da godewa Allah.

Amma kuma sai na ga akasin hakan.
"Haba Nasir me ne ne abin ɗaga hankali a wannan maganar? Ai kamata ya yi kayi murna tunda dai na kubuta."

"Murna fa kika ce kubra? Yanzu kina faɗa min ammiki aure a kan aurena kuma ki ce na yi farin ciki?" Ya faɗa yana nuna kansa.

Sakwato na yi da baki ina kallon sa, na kuma rasa me zance masa saboda gaba ɗaya ya bani mamaki .

Daga haka dai ya fice a gidan ga baki ɗaya.
Haka na cigaba da zama a gidan mu ina kuma jin ɗadin gidan saboda kullum su maryam basma Hadiza suna tare da ni ga su yarima haidar zulfa'u kullu suna nanne da shawuya idan ba makaranta.

Kwana na uku da dawo wa Gwamna ya sa aka kaini asibitin damaturu aka duba lafiya ta nida shawuya muka dawo da kuma alƙwarin da gwamna ya min na bamu gida a dtr ɗin domin mu zauna.
Cike da farin ciki na dawo na sanar da su mama sukayi farin ciki da hakan, sai dai abin mamakin ko kaɗan Nasir baiyyi farin ciki ba. Dan dana gama tsara masa bai ce komai ba ya fice ya barni .

Wani abu da ya ke ɗaga min hankali shine yadda ya daina damuwa da lamari na ya ɗena son ke ɓewa da ni, kuma ko shawuya baya son ɗauka.
Wannan abin ya na taɓa min zuciya! Idan ni yana jin haushi na shi kuma shawuya mene ne na sa?" Na tambayi kaina.

Dan haka sai na fita safgar sa saboda an tabbatar min ina da hawan jini, ban sanar da kowa ba saboda kar hankalin su ya tashi.
Dan haka sai na ɗauke tunani na akan sa dan kar ma na je damuwar sa ta sake sanyawa yawan hawan jinin ya ta'azzara.

Kamar kullum watarana muna zaune dukan mu soja jamil ya zo akayi masa iso har cikin gida ya ke sanar min gwamna ya sama mana gida wanda zamu zauna har da su mama fedo, gidan kuma yana jere ne a layi ɗaya kuma ya mallaka min su.
Farin ciki har da ƙwalla ta haka su mama ma suka yi ta farin ciki da jin labarin, amma Nasir ko ta ri baiyyi ba har muka gama dukkan bidirin mu sai da baba Bala ya yi masa magana tukunna ya ce Allah ya sanya alheri.

Fita ya yi waje aka umarci basma da ta yi masa ra kiya tunda dai ita da yarima sune suka san shi. Murmushi ta yi bata ce komai ba ta bi bayan sa.

Bayan sun fita ne ya ke sanar mata abinda ya ke zuciyar sa game da ita.

Bata ce komai ba ta dawo gida da gudun ta kasan cewar ita ce ƙaramar mu, dan haka sai ta ji kalmar ta yi mata nauyi.

Bayan mun ƙe be ne a ɗakin kwanan mu na ke tambayar ta tsakanin da ta shi akwai wani abu ko babu, amma sai tayi min shiru ya yinda Hadiza ta ce , " Wallahi aunty ba banza ba fa wannan yaƙe haƙwara da ya ke mata kawai ta faɗi gaskiya."

Hararar wasa basma ta yiwa Hadiza tare da kunshe fuska cikin hijab. Shi kuwa yarima da yaga ta ƙi magana ya ce, "Mommy yana sonta fa ɗan yau har ya faɗa mata ɗazun da muka raka shi."
Ya faɗa yana dariya. Jin batun yarima ya sa ta tashi ta gudu ɗakin mama fedo .
Dariya sosai mukayi Maryam ta dubi yarima, "kai kuma wato harda gulma ka yiwa aunty

basma ko? Ai nan gaba bazata sake neman raki yar ka ba wurin soja."

Dariya ya yi ya ce, "Ai kaka zai ce ta je dani."
"Sai na ce masa ka zama mai gulma ai."

Dariya duka mukayi wan da ya yi dai da da zuwan mama fedo ta shigo tana faɗin, "Mai yaran suke shiryawa ne suka wa re ni gefe."

Murmusawa na yi na ce,. "Mama muna shawarar auren autar ki ne."
"To bari na koma wurin auta kuyi shawarar."
Ta mayar da ƙafarta waje."

Sauri na yi na ce "A'a mama mungama ki shigo."

Murmusa ta yi ta shigo ta zauna muka ci gaba da hira har dare ya raba. Anan ne kuma suka bani labarin yadda yarima ya ku buta.

Na yi farin ciki sosai da irin yadda ba fulata na ta riƙe min amanar da na bata, kuma na yi akwarin in sha Allahu zai kai mata ziyara idan na warke.Bayan kwana biyu baba Bala ya sa me ni da batun ya kamata na koma gidana idan na yi kamar sati kuma sai mu fara shirin koma wa dtr ɗin.
Ban ƙi ta shi ba na ce in sha Allahu zan sanar da Nasir ɗin.

To amma Ni har fargabar yiwa Nasir magana na ke akan ko ma war , tunda dai na ga dukkan yadda ya ke son na koma gidan yanzu ko zancen ba ya yi .
Kuma bai sake ce min yau she zan koma ba.

Amma duk da haka na ɗaure na sa me shi da maganar bayan ya zo sun gaisa da baba Bala na sa haidar ya tsayar min shi, saboda idan ban tsayar shi ba nema na ma ba zayyi ba zai wuce.

Abin mamaki abin ɓaƙin ciki shine kalmar da ya furtamin wacce sai da ta afka Chan ƙasan zuciyata.

Har ma na yi da na sanin yi masa maganar.

Ina ce masa nasir ya kamata gobe na koma kafin mu tare sabon gida ya aika min da wata harara, amma duk da haka sai na ce da shi "Yaron nan har yau ba shi da suna balle yanka yaushe za'ayi masa?"
Cike da izza ya dube ni ba ko kunya ya ce, "Kubra! Wallahi ba dan na san kina da ciki ba kika fita Allah da wannan yaron ba wa bane ni sam......"
Ya faɗa yana yarfe hannu.

Cike da bugawar zuciya na kalle shi har wasu hawaye masu zafi na ce, "Nasir! Kasan mai ka ke faɗa min kuwa ...........a fusace ya juyo cikin masifa.............

PG 25

Cike da mamakin maganar ta sa ta tsaya min cikin zuciyata! "Haba Nasir wai me ya ke damun ka ne? Me ya sa kake min haka ne? Nasir ko ka daina sona ne ban sani ba?"

Na ƙarashe maganar cikin sautin kuka.
Kallona ya yi ya zauna gefen wani itace, "Kubra lafiya kalau nifa amma wallahi gaskiya zan sanar miki tunda kika ce kinyi aure kan aure na wallahi ina da shakku a zuciyata! Saboda taya zan yi farin ciki da matar da ta haɗa jiki da wani bayan ta na da aurena? Haba kubra kimin adalci mana idan na ce miki har yanzu kina zuciyata zaki yadda."

Wani irin tashin hankali ne ya riski zuciyata na kalle shi na sake kallon sa cike da mamaki! "Nasir yau ni ce ka ke gudu? Nasir ka mance irin tarin ƙaunar da na ke maka ne?"

Ban bari ya ji wani bayanin na ba na juya cike da ta fasar zuciya na shige ɗakin su basma,har wasu taurari na ke gani suna hana min ganina sosai.
Gadon na faɗa na kwanta ina wani irin kuka mai tsuma zuciya.
Shi kuwa gidan sa ya wuce cike da damuwa domin har ransa ya ke jin ba ɗaɗi akan abinda ya min, amma kuma idan ya tuna kalaman sadauki abokin sa, sai yaji kawai ko ma mai zai faru ya faru.

Ganin halin da nake ciki ba mai ɓullewa ba ne yasa na fara sanar da mahallici na halin da na ke ciki, saboda shine gatana a duniya da lahira.

Haka baba ya maida ni gidan Nasir ba tare da jin ta bakina ba.
Bai ce komai ba ganina a cikin gidan sa tare da yaran sa, dan haka nima na cigaba da zaman shirya kayan ƙaura zuwa dtr ɗin haidar ne ya ke taya ni haɗa kayan ya yinda yarima ya ke ta yiwa shawuya wasa sai ga basma ta shigo.
Da farin ciki na tar ɓe ta ta zauna ta da fa ka faɗata.
"Aunty za'a koma binni."
"Basma kamar ban taɓa zaman gashuwa ba?" Na faɗa ina riƙe haɓa .

Dariya sosai basma ta yi. "Aunty yanzu dan Allah taya zaki haɗa gaashuwa da dtr kuma?

Taya state da local government zasu yi ɗaya?"

"Basma ke nan ni a wurina duk ɗaya ne fa tunda dai rayuwar gayu ce kuma nima na iya ɗaukar gayun ba shike nan ba."

"A'a aunty duk dahaka sai kin kula sosai kar su gane ke y'ar ƙauye ce su raina min ke, kin san su da jiji da kai fa mutanen dtr."
"Haba ke kuwa ai kowa kika gan shi wuri to tilas ya san yadda zai zauna da ma'abota wurin domin gujewa raini, karki damu."

"Yawwa aunty na haka na ke son ji ."

Sai wajen dare muka gama haɗa kayan duka muka loda su gefe cikin gidan, kwansilik basma ta yi mana wanda yarima ya taya ta cura mana yaji jajjage ya sha manja sosai yaji komaibya sha maggi, har da salat ta yanka mana a ciki .

Bajewa mukayi muna haɗiɗiyar sa basma ta kunna waƙar salim smart na Allah ya jiƙaina idan har ba ke wa'adin rayuwata ya zo karshe. Rerawa ta ke tana cin dan sulut din kamar ita tayi wakar kallon ta na tsaya yi har sai da ta fara min dariya. Ta ce " Aunty wai dan Allah ki daina kallona."

"Bazan daina ba basma, Wato irin kin fara soyayya ɗin nan ko? Shine kike nuna min."
Na faɗa cikin zolaya.

Kunya ce ta kama ta sai ta rufe idanu kasan cewar ta mai kunya sosai.

Bayan sati guda da komawa ta ne muka haɗa komai mu da su mama fedo da baba Bala da basma mukayi ban kwana da jama'ar garin mu ba tare da sun san garin da zamu koma ba.
Saboda tsaro.

Mun sauƙa lafiya gida kuma ya yi masa Allah a anguwar sabon fegi ya ke kusa da ladabi suya.

Gidan su mama gida ne mai dauke da ɗakuna uku da falo a tsakiya wanda ya ke kunshe da toilet a kowanne ɗakin sai karamin kitchen da kuma wani bayi a waje da kuma tankin ruwa babba.

Haka gidan da na ke ya ke shima sai dai shi har da wajen ajjiye mota da kuma wurin dinning table.

Farin ciki gaba ɗaya ya bayyana a fuskokin mu amma banda Nasir .

Kwanan mu uku ya koma kananma ya ce zai je ya dawo.
Amma shurun sa har wajen sati biyu kuma layin sa baya shiga.

Kwatsam basma ta na zaune a kayi sallah ma da ita tana fita sai ga Captain jamil, dan haka na ce ta yi masa iso kawai falona .

Bata ɓata lokaci ba ta sauke shi kuwa, yarima ya je wurin sa suka gaisa saboda dukkan sanda ya zo sai ya nemi shi, ya ce yana matukar kaunar sa.

Amma bazan mance kalaman da na ji jamli ya na faɗawa basma ba wanda har suka sanya ni kasa tsayawa ya tafi na ji gaskiya lamari.

Har sai da na fito wurin da suke zaune..........

PG 26

Fitowa nayi ina riƙe da baki tsabar mamakin abinda na ji jamil ya na faɗa, ban yi ƙasa aguiwa ba na doshi wurin su , amma kuma sai na ji bai kamata ba kawai sai na waske na yi hanyar da zata sada ni da kitchen.

Koda na shiga kitchen ɗin mu kasa taɓuka komai na yi tsabar farin cikin da ya mamaye min zuciyata, Allah dai ya sa kunne na dai dai ya ji min ba zolayata ya ke ba.
Aikin dole na kama yi ganin bai dace na sake koma wa ta gaban su ba.

Kusan awa guda ina zaune cikin kitchen ɗin tukunna na ji fitar su a falon dan haka da sauri na dawo falo na zauna ina tsumayin jiran basma.
Bata jimaba ta dawo cike da farin ciki a kan fuskar ta.
Kasa jure nawa farin cikin na yi na mike na same ta tare da riƙe hannun ta na ce, "Basma, sanar da ni dalilin da yasa kike farin cikin nan."
Murmushi ta yi, "Aunty sai kin bani tukuici tukunna."
Murmushi na yi na kalle ta "Karki damu zan baki."

"To aunty shike nan, na san ma kinji ai amma dai bari na sanar Miki. Gwamna ya. Ce da ke da baba da mama fedo bana azumin sai a Saudiyya."
Ta faɗa tana rungume ni.
Sa ke rungumeta na yi muka yi ihun murna har sai da su haidar suka fito a ɗakin su suna kallon mu.
Suma da muka sanar musu murna suka hau, yarima kuwa har da rawa wai zan kawo masa bindigar roba da mashin.
Haka dai muka yi ta farin ciki nida yaran daga ƙarshe muka ta fi gidan su mama muka yada zango.

Mama da muka sanar mata harda hawayen farin ciki. Baba ma ya yi farin ciki sosai
Sai dare muka koma gidan nida basma ita ce muke kwana tunda Nasir bai dawo ba.

Zama na yi bakin gadona na dauki wayata na fara gwada layin Nasir na waya amma shiru baya shiga, na gwada ya kai so biyar amma amsar ɗaya ce.
Haka kurum na ji zuciyata ta yi min zafi, na so ace wannan farin cikin da Nasir zamuyi shi. Amma ya maida kansa ge fe, kuma hakan ya yi mugun tsayamin a zuciyata.
Saboda tsawon zamana da shi bamu taɓa samun saɓanin da zai kai ya yimin yaji ba, amma yanzu ya yi min a lokacin da na fi bukatar sa a gefe na.
Haƙiƙa ina kaunar Nasir domin zamana da shi ma ya fi ƙarfin a ƙirashi da soyayya sai dai ƙaunayya.
Amma ga shi yau ya juya min baya, baya ko tausayin halin da na ke ciki. Ina amfanin kishi akan abinda baka da tabbas.
Na ƙarashe maganar tare da goge hawayen da ya ɓurtso da ga Idanuna.
Ban san ya zanyi da shi ba ya daina guje min da zanyi, shi kuma ya gaza fahimta ta. Ya Allah ka shiga lamarin wannan zaman na mu.

Amin na ji basma ta faɗa tare da da fa ka faɗa ta.
Dago idanuwa na yi na dube ta .
Ban ce komai ba na sake sunkuyar da kaina ƙasa .
Wuri ta samu ta zauna ta ce, "Aunty wai yanzu har fushi Nasir ya ke Miki? Duk irin halin da kika shiga bai gani ba? Ko da kuwa a ce auren da a ka Miki wani abu ya faru ai ya kamata Nasir ya yi haƙuri."
Shiru na yi na wani lokaci Sannan na ce.
"Basma haka ƙaddarata ta zo ni kuma da ga wannan gangamin sai Wannan.
Amma bana son su mama su sani kinji ."
"In sha Allah aunty ba wanda zai ji, kuma Allah zai kawo Miki mafita da wuri."
"Allah yasa haka my lovely sister na."

Bamu jima ba gwamna ya turo a ka je da mu muka bada passport a kayi dukkan shirin da ya kamata saboda ba zamu jima ba zamu ta fi.
Kananma muka je mukayi sallama da 'yan uwa da abokan arziƙi sannan muka wuce gashuwa nan ma mukayi sallama da 'yan uwa.
Sai da ya zama saura kwana uku tafiya Sannan Nasir ya dawo dtr.
ba yabo ba fallasa, saboda yana kula yaran sa ba kamar baya ba da su ma ya yi watsi da su.
Amma ta fanni na ba abinda ya sauya hatta shimfiɗa idan muka hau Chan ƙuryewar gado ya ke wuce wa ya kwanta. Ban taɓa yi masa magana ba saboda ina jira na ga gudun ruwan sa.

Ashe kuwa ruwan na sa yana mugun gudu ne da tozarci da yaudara har ma da rashin sanin daraja ta.

Wannan ruwan na shi ya yi guda da zuciyata fiye da yadda nake zato.

Kuma shine abu na farko da Nasir ya min na ji ma tsane shi a duniya tsana mai yawa.......

PG 27

Sai da lokacin tafiya ya rage saura awa biyar, sannan ya ce dani yana son muyi magana.
Cike da farin ciki na sa me shi ina fatan maganar da zamuyi ta kasan ce alkairi murabu cikin kewar juna.

Amma kalaman da yazo min da shi ya tarwatsa dukkan tunani na.
"Kubra, ina son ki ajjiye hankalin ki da kyau ki saurari abinda zan faɗa miki ciki lumana."
Ajjiyar zuciya na sauƙe cike da damuwa saboda yadda na ga fuskar sa na san tabbas akwai damuwa.
"Ina saura ranka mijina."
Na faɗa cike da fargaba da neman sulhu.

Sa ke tamke fuska ya yi ya ce, "Magana ce akan tafiyar ku a matsayi na na mijin ki sai dai ki zaɓa, tafiya umara ko kuma zaman auren ki! Wanne kika ga ya fi miki, ya rage na ki."
Kamar sauƙar aradu naji sautin maganar ta sa har cikin kwakwalwata.
"Nasir me na maka haka? Wanne laifi na ke da shi a wurin ka?
Shin Nasir ashe lokacin Zaizo ka tsaneni irin haka? Yanzu tafiya Makkan ne ka ke min ɓakar maganar a kan ta?"
Duka na jero masa tambayoyin .
Shi kuwa ko a jikin sa bai wani damu ba ya sake kishin giɗewa a jikin gado, wani takaici ya kama zuciyata kamar na shaƙo sa na kama duka! Dan haka cikin ƙaraji na tashi ina huci na ce,
" Kayi dukkan abinda ka ga yada ce! Tunda dai haka ka ce!"
Fuuu na fice na bar masa ɗakin.
Bai ce dani uffan ba har na bar dakin, falo na je na zauna na fara rero sabon kuka kamar wata amaryar da ake son rabata da iyayen ta.

Ana haka su mama fedo suka zo ita da su Maryam saboda na musu alƙwarin da safe Zanje ban je ba kuma shawuya baya jin daɗi shine suke tunani ko jikin ne .
Ganin halin dana ke ciki sai sukayi turus! Suka tsaya, waskewa nayi na fara ƙokarin goge fuskata kamar ba komai na ce dasu su ƙaraso mana, shigowa sukayi suka zauna duka jikin su ya yi sanyi. Mama ce ta ce, "Kubra, me ya faru? Lafiya kike kuka?"
Shiru na yi bance komai ba saboda bani da abin faɗa, chan kuma sai dabara ta faɗo min, "Mama wallahi idan na tuna wahalar da na sha da yadda rayuwa ta bani wahala nida yaron nan sai dai na ji hawaye yana zuba daga idanuna."
Na shimfiɗa musu wannan ƙaryar kawai don bana son su san halin da muke ciki. "

"Haba kubra me sa zaki sa ka kanki cikin damuwa bayan kuma kin samu 'yancin rayuwa. Don Allah ki dena, saboda zaki iya kamuwa da cuta idan har zakina bibiyar Abun arai."

Kalaman mama ke nan da suka faɗa cikin masarrafin jina.

"In sha Allahu mama zan ki ya ye hakan."

Na bata amsa cikin sanyin murya.

Gefe guda kuwa su basma Maryam Hadiza ne duka suka zauna kusa dani duk sunyi kalar tausayi.

"Yawwa kubra Allah ya muku albarka dukan ku."

Da Amin muka amsa mata.

Sannan ta ce dani idan Nasir yana nan tana son suyi magana da shi.

Dan haka kai tsaye na je na sanar da shi ba tare da na tsaya na saurari abinda zance ba.

Bai jima ba ya fito yana murmushin munafurci yana gaida mama kamar ba shi ba, dukan su suka gaida shi cikin sakin fuska illah basma da tasan halin da ake ciki.

Har da yiwa mama fatan zuwa ayi a sa'a kamar ba shi ne ya gama min tijara a ɗakin ba.

Mama ta dube shi. "Nasir Yakamata a yi wa yaron nan suna kafin mu tafi.Sunkuyar da kai ya yi ya ce, "In sha Allahu mama zuwa gobe zan saka masa."

"Yawwa Nasir, Allah ya maka albarka."

Da amin ya amsa ya miƙe ya fita .

Hakan kuwa akayi ana gobe ta fita ya ce da mama sunan yaro Ahmad ya yi masa sunan rana ba takwara ba ne .  Na yi farin ciki sosai duk da cewa bai kawo abin yanka ba, abinda yasa bai dame ni ba kuwa shine, sunna ce mai ƙarfi, ba waji bane sai anyi. Kamar yadda wasu suke ɗaukar cewa dole ne har ma idan ba ayi ba ana dauka kamar an aikata sa ɓo.

Haɗe dukkan kayan mu mukayi domin asubar fari zamu tafi Kano Chan zamu hau jirgin yamma.

Nasir na samu yana kwance yana latsa wayarsa yana ta famar sakin murmushi ga dukkan a lamu chat ya ke yi abin sa.

"Ina son magana da kai ."

Sai dai na furta ta sau uku sannan ya ce "Ina jinki."

"Nasir na zaɓi ta fiya Saudiyya idan har yanzu kana kan bakar ka, domin ba zan taba cewa su mama bazan tafi ba saboda ka hanani.

Amma idan zaka iya sanar musu da kan ka sai na haƙura."

"Allah Ya tsare hanya ."

Shine ka ɗai abin da ya furta min ya juya ya kwanta abinsa."

Ba yabo ba fallasa na ɗan ji sauƙin damuwar da ta ke cikin zuciyata.

Cike da farin ciki jirgin mu ya ɗaga zuwa Saudiyya.

Ibada muke cikin farin ciki da kwanciyar hankali kullum sai munyi waya da su basma da Maryam da Hadiza, a wurin su na bar yaran nawa dukan su.

Kwanci ta shi asarar mai rai bamu yi aune ba har watan Ramadan ya zo karshe amma da yake anan zamuyi sallah, wayar da mukayi yau na ji Muryar basma cike da damuwa amma kuma na yi nayi ta sanar min komai amma sam ta ce ba komai.

Dan haka hankali na ya yi matukar tashi da zaƙuwar zuwa gida. Shigar yamma mukayi wa dtr dan haka har wani sauri nake na kai ga gida.

Muna shiga na ga wata mata hakimce kan kujerar falona, Nasir ya na gefen ta suna shan dariya saboda kallon da suke yi a waya ya ɗauke masa hankali.

"Nasir! " Na furta cikin ɗaga murya sosai.

Firgigit! suka juya suka kalle ni.

Idanun sa kawai na kallah na ga tsan-tsar rashin gaskiya a idanun sa.........

PG 28

Sororo ta yi matar ta wani yatsina fuska tana faɗin, "Baby wai yau daman zata dawo ne baka sanar min ba?"

Kallon ta ya yi ya kasa cewa komai ya sake kallona ya fara yaƙen dole yana faɗin, "Har kun iso ne?"

Ban kula shi ba na wuce ɗakina kai tsaye ina jin kamar na shaƙo shi na yi ta duka har sai na ga baya motsin kirki na bar shi, amma kuma wata zuciyar tana ta bani hakuri.

Biyo ni ya yi ɗakin ya zauna bakin gado ya ce, "Kubra bayan kin tafi abubuwa da dama sun faru kuma wal........" Hannun da na ɗaga masa ne ya sa shi yin shirun dole, "Bana son jin komai Nasir daga gare ka! Kawai abinda na sani shine tunda dai gida nawa ba naka ba ko? To ko matar ka ce ko ma ƙaruwar ka ce ka fita min da ita ayu ba sai gobe ba!"

Ina hana fadar haka na wuce toilet ɗin da ya ke cikin ɗakin na rufe na fara kuka mai cin zuciya.

Shi kuwa daga nan wucewa ya yi wurin matar ya bata hakuri yadda take ta masa masifa ya samu ya bata hakuri ta wuce ɗakin dake gefen nawa wanda a baya shine matsayin turaka.

Gidan mu ya shiga ya yi wa su mama sannu da zuwa gefe guda kuma su Hadiza suna masa kallon banza game da cin amanar da yayi min.

Sai wajen magrib yara suka dawo a makaranta suka mana oyoyo suna ta farin ciki, kayan tsaraba na cire na basu kowa na shi da su jallabiya da su huluna sallayoyi da sauran su.

Kusan tara na dare ya samu baba bala ya ce da shi ya na neman ya fiyar sa ya yi masa laifi amma kuma ba laifi.

Baba Bala ya ce ba komai ya sanar masa, dan haka ya zuƙa masa ƙaryar wai daman ya ce baya son tafiyar saboda bazai iya jurewa ba na ce da shi ya yi aure to shine bayan na tafi ya haɗu wata bazawara suka daura aure harma ta tare.

Baba Bala ya ce ba kamai ai tunda ita ce ta zaɓi hakan, kuma ma sunnar Annabi ce ai Allah ya yi muku albarka.

Ko da baba ya je wa da mama da zancen ta yi matukar mamaki, don ta san halina ba na wani abu ban sanar da ita ba.

Amma kuma ta ce ba damuwa ai tunda ita ce tace ayi hakan.

Ina shiga gidan da safe na samu mama fuskar ta ba walwala, na dube ta "Mama mai ya faru

na ganki haka?"
"Ba komai kubra." Ta ce dani
Sai kuma ta ce.
"Kubra banyi tsammani zaki yanke hukuncin wani abu baki sanar min ba, amma tunda har ya riga da ya faru shike nan. Sai dai ki sanin ki guji zama gida da kishiya gida guda idan ba dole ba, saboda anfi samun matsalar zaman.
Ki na da damar cewa Nasir ya yi aure amma da baki bashi damar haɗa ki ba, ba wai ina zugaki bane ."
Sakwato na yi kamar wata gunki.
"Mama ban gane me kike nufi ba , taya zan bawa Nasir damar aure har da zaman gidana."
Na sanar mata haka.
Murmusawa ta yi ta ce "Koma mene ne ai abinda ya riga ya faru ya faru tunda Nasir ɗin da kansa ya ce kince sai kin tafi sai dai ya kawo wata gidan. Kinga kuwa ai ga watan Allah ya baku zaman lafiya. "

Mama ta faɗa tana gyara ɗaurin kallabin ta.

"Haba mama wallahi bani ce nace masa ba wallahi karya ce yamin kawai! Kuma wallahi bai isa ba! Nidai bamuyi haka da shi ba.
Kuma wallahi yau zata bar min gida."
Na faɗa ina miƙewa tsaye.

Mama ce ta ce na dawo na zauna. Bayan na zauna ne ta ne mi sanin gaskiyar lamari kuma ban ɓoye mata komai ba yadda muka yi da shi ranar da su ka ganni ina kuka a gobe tafiya.
Mama ta jinjina lamarin sosai da sosai ta kuma yi min nasiha da nayi haƙuri na bi komai a hankali.
Zuciyata na ji ta yi min sauƙi na tashi na tafi gidan .
Ina shiga na ci karo da ita tana ta wanin hura hanci ta tura ɗan kwali gaban goshi kamar zai faɗi.
Ta tsare min hanya da gangan dan haka sai na kauce ban kulata ba, amma ta mangaje ni. Kallon ta nayi murmushi ɗauke a kan fuska ta na ce, "Bani wuri na wuce karmashashiya, saboda ke baki kai na haɗa jiki da ke ba shi wancan ɗan tauren da ya ajjiye ki shine sa'a na."
Zaburo min ta yi saboda daman jira take dan haka hannu na sa ha hankaɗe ta gefe na wuce ciki abina.

Ko minti goma ba ayi ba Nasir ya shigo yana huci kamar zai dake ni.
" Duk abinda zakiyi kar ki kuma dukan baby! Idan maganar gida ne kuma ta zo ke nan na fa sa chan jawar!" Ya faɗa yana nuna min yatsa. Shawuya da yake gefe kuwa sai miƙa hannu ya ke kamar zai kama shi yana ta ɓangala dariya.

Cike da masifa Nima na zabura na ce, " To munafiki ! Wallahi baka isa ba sai ka bar gidan nan ɗin kuwa. Ko ba duka ba ! To yanzu na fara. Butulu kawai irin ka. Na faɗa ina mai zama abakin gado ina rusa Kuka.

Fice wa ya yi yana guna guni.
Dan haka na bi shi cikin ɓacin rai har bakin ɗakin Babyn inji shi na ce "Ke baby kike ko ma Babyn roba ce azo a fice min daga gida wallahi ba gidan sa ba ne idan ma bai sanar Miki ba to maza azo a fice min daga gida!"
Na faɗa cikin ɗaga murya jin haka yasa duka suka fito zuwa falon.
Ta zuwa zata min wani iyaye na dauke ta da mari na mai da ita gefe shi ma da yayo kaina na hankaɗe shi na yi ya faɗa kan kujerar da ke bayan sa.
Saboda kamar wata zaki na ke jin kaina a lokacin.
Ganin na burkita su da masifa ina shiga ina jefo mata kayan ta zuwa falo yasa ya fice ban san mai ya shirya ba sai da na ga baba Bala har gida ya shigo ransa a matukar ɓa ce...

PG 29

Sai da hantar cikina ta kaɗa ganin irin kallon da baba ya ke je fo min da shi, ita kuma makirar tana ganin sun shigo ta zuɓe ta kama ihun ƙarya tana cewa wayyo cikin ta.
Baba Bala kai tsaye inda na ke ya nufo ni kuma na sunkuyar da kaina ban yi tsammani ba na ji an wanke min fuska da marin da rabon da na sha shi irin sa har na mance,.
Cike da mamaki na ɗago idanun da suka rine min zanyi magana amma baba ya hanani sam! Ta hanyar ɗaga min hannu. Dan haka dole na haƙura da maganar naa durƙusa a wurin ina sauraran abin da zai ce.
"Ke da kanki ki ka umarci mijin ki da ya ne mamaki abokiyar zama kuma a gidan ki, dan haka wallahi baki isa ba zama yanzu ta fara a cikin gidan nan! Kar ma na sake jin wannan batun na faɗa miki.
Daga haka ya juya ya fice a gidan, ita kuma ta mike ta min gwalo ta shige cikin ɗakin ya rage daga ni sai Nasir.
Duban sa na yi cikin kuka na ce,
"Kai kuwa mai na maka ka maida zaman auren mu haka? Mai na tare wa rayuwar ka? Wai wanne laifi na maka wanda har ya kai ka saka min da wannan butul cin?
Kasan irin gwagwarmayar da na sha domin kare mutuncin ka? Ka san faɗi ta shin da na sha kuwa? Nasir mai yasa ka zama butulu mai bakar zuciya? Ka mance irin soyayyar da take tsakanin mu? Haba Nasir ka tausayawa rayuwar mu mana ko dan yaran ka."
Na ƙarashe maganar cikin kuka.
Bai ce dani uffan ba ya bini da kallo yana mai shigewa ɗakin matar sa.
Bayan na gaji da tsayuwar nima na shige nawa ɗakin ban sake fitowa ba har sai da yarana suka dawo gidan tukunna.
A falo muka yada zango muna karatu nida su amma ba ko kunya Nasir ya leƙo kai ya ce mu rage murya muna damun su.
Bance ƙala ba ban kuma kalle shi ba.
Haidar ne ya ɓata rai ya ce, "Mommy wai kawai dan daddy ya yi aure sai yana mana haka har da ke kuma."
Harara na banka masa dole ta sa ya sunkuyar da kansa ,
Na ce "Haidar baban ka ko me zayyi fa baban ka ne dan haka bana son na ji wani ƙorafi ya fito

daga bakin ka indai har akan baban ku zakayi shi."
To ya ce badan ya so ba na ce dasu mu tashi mu shiga cikin ɗakina kawai muƙarasa karatun, haka kuma mukayi a chan muka gama har lokacin sallah ya yi.
Haka muke ta fama da rayuwar mu ni da yarana a cikin gidan nice da gida sune da isa ita kuma mandiyar ta sa ta samu ɗaurin gindi sai yadda ta ga dama ta ke yi a gidan.
Rayuwa mai tafiya ce kamar wasa har an sanya lokacin bikin basma da Captain Jamil, Haka su Maryam ma sun fidda mijin aure Ita da Hadiza saboda duka za ayi bikin a ta re.
To dan haka duka hankali na yana kan hidimar bikin ne a matsayina na babbar yayar su, Basma kuwa cewa ta ke ita wallahi aure ya fita kanta saboda yadda Nasir ya juyamin baya duk da irin soyayyar ta ke tsaka nina da shi .
Zaunar da ita na yi har ma da su hadiza ɗin na ce musu, "Shi fa aure da kuke ganin sa daman ya ga ji ƙalubale a cikin sa kuma kowanne bawa da ƙaddarar sa a rayuwa, dan haka kuyi ta addu'a Allah yasa mazajen da zaku aura su zama haske a cikin rayuwar ku.
Kuma daman dole shi aure wani zama ne na a sa ɓa kuma a gyara ba wai zai kasance irin soyayyar layi ba ne.
A'a ya danganta da kalar mijin da kika aura din. dyan haka kuyi hakuri da mazajen ku a ko wanne hali shi yasa zaku ji motsi kaɗan ance sai hakuri fa wance, to zaman auren ke nan daman .

Kuma in sha Allahu ina muku fatan alheri a rayuwar ku baki ɗaya." Duka rungume ni sukayi suna kuka wai su wallahi ba su son rabuwa dani.

Dariya na yi musu saboda sun fara da wuri na shige toilet ɗî na na barsu a wurin zaune.
A ɓangaren Nasir kuwa ba abinda ya sauya daga gare shi a halin sa da matarsa .
Amma kuma duk da haka ban rasa komai ba saboda dukkan wani abu da ya samu na taimako jama'ar hijira to gwamna baya mance wa dani har ma da shi kan sa, ba kama layi ba shan wahala namu har gida yake zuwa mana, kuma hakan ya na samuwa ne daga gwamna saboda yana duba wahalar da na sha .
Shi yasa a rayuwa ba zan mance da gwamna *mai mala buni* ba saboda ya min alheri masu mugun yawa a rayuwata .
Da irin taimakon da na ke samu wajen sa na samu na fita kunyar auren ƙanne na.

Biki ya kusa na shirya komai na gyaran jiki domin kuwa wurin shahararriyar mai gayran jikinnan na kai su dukan su wato UMMU HEEBBAT ta gyara min su da kyau ciki da waje kama da kan turaren da amarya ya kamata ta turara a cikin jikin ta da kuma jikin ta waje da abinda zata sha ba mai cutarwa ba masu inganci ba wanda kuma ya fi karfin su ba,saboda wani lokaci ana bawa amare maganin uwargida garin gyara, to ta ina zaku hada maganin da wacce ta saba da wacce yanzu zata fara zai zama guda? Shi yasa da zarar ankai amare zasu fara rawar ƙafa jira suke kawai azo wurin.
Tunda an gama haukata su, to ita Ummu HEEBBAT tana kiyaye hakan .
Dan haka sun sha  gyara sun fito sai ta shin ƙamshi suke ga wani yalƙi da suke kamar sabin babys, kuma duka wannan aikin Ummu HEEBBAT ne.
Haka har Allah ya kawo mu ranar bikin dangi kowa ya hallara har da jama'ar gashuwa da

kananma  duka sun hallara a dtr an sha biki cikin farin ciki kuma dukkan su suma ba a gari bane. basma   gashuwa aka kaita saboda jamil ɗin a chan ya ke aiki.
Mun sha kukan rabuwa da basma saboda mun fi kowa shakuwa da ni da ita.
Har ɗakin ta na mata raki a garin gashuwa, kuma na samu jamil na bashi amanar ta da kaina saboda kaunar da na ke mata ta daban ce.
Da kyar muka rabu ranar da zamu dawo dtr ɗin  an sha fama tukunna.
Amma tijarar da na tarar Nasir ya shuka min a gidan sai da na ji dama ban zo ba.
Kuma na saka a raina daman saboda baba Bala ne nake daga masa kafa amma tunda ya bi mutanen kananma duba gonar sa dan haka na ce yau za'ayi dukkan masifar da za'ayi agidan koda kuwa karshen zamana da shi ya zo..........

PG 30

Last book 1

Kallon kallo muka tsaya yi nida Nasir na ce, "Me zan gani haka? Nasir nida gidana har ana min waje da kayan ɗakina."
Na ƙarashe maganar ina nuna kaina.
Amaryar sa ce ta zabura ta ce, "Eh haka na ke so wannan ɗakin zan koma idan kuma da gaske gidan kine kamar yadda kike tun ƙaho sai ki hana mugani. " Ta faɗa har tana wani kaɗa jiki da hura hanci.
Nasir ɗin na kallah, "To ka sanar mata gaskiya a kan gidan idan ma ka ce mata naka ne kuma yau dole wannan ta bar gidan tunda ba gidan tsoho be ne ! Nasir na gaji da rainin hankalin da kake min a cikin gidan nan dan haka wallahi yau ko da zai zama silar rabuwar mu da kai sai ta bar gidan nan yanzu ba sai an jima ba."

Na faɗa ina sauke lumfar-fashi saboda ban saba da masifa ba sai da ta riske ni .
Kallona ya yi ya watsar ya je wurin amaryar sa ya ce da ita, "Baby kiyi haƙuri bata da hankali kinsan duk wanda yayi zaman daji kansa sai ahankali, gida kuma karki kula ta da wannan shirmen nata da ta ke yi gida dai kin shigo ke nan sai mutuwa."
Sakwato na yi ina al'ajabin kalmar shi ta zaman daji ban san sanda zuciya ta zare ni ba na dauƙi wani takalmin sa sawu ciki na kwada masa a bayan sa ita ma na buga mata a kai na ce, "Hauka ka ce ba? Yanzu zaka ga ainahin Hauka ! Fuzgo ta nayi tana ƙokarin kai min duka na buga ta da bango ta fasa ihu! Ganin jini ya ɗan ɓullo a goshin ta sanadin gorjewa tuni ya yi kaina ya lafta min mari tare da faɗin na sake ki kubra! "
Chak! Na tsaya da komai na ji kalmar har cikin jikina duk kan gaɓoɓin jikina sai da suka amsa kalmar.
Wani tashin hankali ne ya ziyar ci zuciyata saboda ban taɓa jin wannan kalmar a zaman mu

ba sai yau.
Cike da damuwa na ɗaure zuciyata na haɗiye kukan da yake shirin to na asirin zuciyata na ce, "Na ji na gode sosai amma yanzu abarmin gida!"
Take ya fara wani borin kunya dan haka ba yadda zayyi da ni ya ce, "Baby zo mu tafi idan manya sun shiga lamarin ta barmin gida!" Da wannan yaudara ya samu kanta suka haɗe dukkan kayan su suka fita suka barshi a wurin.

Ɗakina na shiga na zauna bakin gado na fara rafsa kuka saboda wallahi har zuciyata ina ƙaubar Nasir ban taɓa tsammani zai sake ni saboda wata ba, sai gashi yau ya ƙaryata zuciyata da gurbataccen tunanina.
Har ma nayi dana sanin shiga harkar sa.

Sai wajen awa biyu suka zo da mai jega ya kwashe musu kayan su ya jefa min shaidar sakin ya yi gaba abinsa.
Bayan na sha kuka da godewa Allah akan irin tawa ƙaddarar nazaci bayan gangamin da na sha a dajin idan na dawo gida zan samu salama ashe da ma nayi zamana da sabon mijin da na aura a dajin wataƙila tunanin yarana da iyaye ya sa na zama mai gajeren kwana na mutu na huta!
Sai dai kash! Bakin alƙalami ya bushe, aikin gama ya gama.
Koda na je wa da mama da batun ta min faɗa sosai amma kuma ita da kanta ta ga rashin kirkin Nasir da abinda ya min,kuma ta ce dani idan har ya zalunce ni na zuba idanu tun a duniya zai ga sakamakon sa.
Haka na ci gaba da zama da yarana har tsawon watannin uku kuma koda baba ya dawo bai wani ɗauki zafi sosai a kaina ba.
Dan haka na dan samu sukunin rayuwa ya yin da shawuya ya ke da shekara uku a rayuwar sa .
Ba laifi ya zama lukuti duk da cewa gaba ki ɗaya shayarwar sa  na yi ne cikin tashin hankali.

Su yarima da haidar kuwa yanzu suna jss 2 ya yinda zulfa'u ta ke primary 4
Ba zato ba tsammani watarana muka tashi da wata mutuwa wacce ta yi sanadiyar shigar dukkan dangin mu tashin hankali wanda idan kuka cire mama da baba to bawan da ya kaini tashin hankali kai wani lokaci ma har gwanda su mama da baba tunda suna zaune saɓanin nida hankali na ma ya gushe.
Tunda dai da zarar na dago kai idan na tuna cewa babu basma a cikin duniyar da na ke sai na sake sume wa,a Gaza gane wa yake dan dama dama tsakanin nida jamil, kamar akan mu aka fara mutuwa.
Na shiga wani yanayin da har sai da aka fara sallama rayuwa ta tunkunna na dawo ɗan kaɗan

Na sha jinya na lalace amma bayan wani lokaci na samu nutsuwa har ma na fara fita aikin da gwamna ya sama min wanda ya samu ne a lokacin da bani da lafiya, an yi shine amin bazata amma kuma da aka zo aka tarar bana hayyaci na.
To da na dawo normal kuma sai na fara rayuwa kamar komai bai faru ba duk da dai cewa

akwai tabon a zuciyata.
Ji na nake kamar wata sabuwa yadda komai ya ke guda cikin rayuwarmu nida yarana lafiya.

Amma dawowar Nasir cikin rayuwa ta, da irin kashin shanun da ya shafamin a fuskar dukkan wanda yazo aure na, shine tashin hankali da ya zama barazana ga rayuwa ta har ya kai ga jama'ar da muke tare duka suna baya baya dani.

Ban gama sanin Nasir mugu bane sai da ya min wani mugun sharrin wanda duka duniya ta ɗauka ya barni cikin halin ni 'yasu........

Alhamdulillah anan na kawo karshen book1

In sha Allahu zuwa wata na biyu a sabuwar shekara wato fabarairu zan zo muku da na biyun sa

Ku kasan ce dani ta ku Ummu HEEBBAT.

Ina muku fatan alheri fans a duk inda kuke na gode sosai da yadda kuke min addu'o'in alheri saboda wannan littafin

Ƙarshe.